700.000 F — 655.000 F = 45.000 F
Ciniki-uwa=riba

In huhu 19 aka saida:
665.000 F — 655.000 F = 10.000 F riba kaɗan
In huhu 15 aka saida
35.000 F × 15 = 525.000F
525.000 F – 655.000 F =—-130.000 F faɗuwa

Ciniki-uwa= faɗuwa

Idan ana son a ci riba

1. a yi lissahi tun farko a gano in an hidda uwa in riba na shigowa.

2. a sayi goro mai yawa dan yan kacare kowa ya samu

3. a adana da kyau kar a yi sake ya bushe.

4. a bar saidawa bashi, wasu in su ɗauka ba su biya.

5 wannan sana'a na bada damar a ciyar da iyali har a yi wasu buƙatu na lakkwal, abinci, tufaya da sauransu..

Maza ke yin wannan saboda suke da isassahen jari da mutane masu iya daukar goro.

| | |
|---|---|
| lamba | TG12 |
| Sana'a | Sana'ar busassar tumati |
| Gari | Kalhu.G.tudu |
| Kala | Sana'ar saida kayan gona |
| Sunan hausa | Sana'a busassar tumati (kodo) |



| ƙaya | Yawan kaya | kuɗin saye | Kuɗin saidawa |
|---|---|---|---|
| Tumati kodo | Buhu 40 na tumati kodo | 400.000 F | 480.000 F |
| jimilla | | 400.000 F | 480.000 F |

Hanyoyi . ina cin kasuwanci gidan Tudu, Gidan gara, alibu da ashanabu amadu dan in sayo kodan tumati busassahe wajen manoma masu kawo shi: sai in kawo shi nan Galmawa in saida ma yan kacare ko masu ci.

Yadda ake saidawa:



Ana saida kodon a aune

A yi tunani tun kahin a soma sana'ar saboda a sami in ana iya hidda uwa har a ci riba.
kuɗin sayen kaya: 400 000F
20 000 : na kuɗin mota
20.000F na takis
1000F na dako
Jimilla kashe-kashe= 423.000 F
kuɗin saisuwa : 480.000F

Idan duka aka saida
480.000 F – 423.000F = 57.000 F riba

In an saida kashi 89/100
427.500 F – 423.000 F = 4.200 F riba kaɗan

In kashi 80/100 aka saida
384.000 F – 423.000 F = - 39.000F faɗuwa

Idan ana son cin riba
1. a yi nazari tun da farko dan a san uwa na hitowa har riba ta shigo.

2. a adana tumati kodo da kyau

3. a sayi kodon da yawa ga kakarshi a aje da kyau.

4. wannan sana'a ana cida iyali da ita har a biya masu lakkal, abinci da tufafi.

Kundin sana'o'in hannu : Mai yin aiki da kanshi

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP01 |  |
| Irin sana'a | Sabunin wanka | |
| Gari | Kewayen garin yamai | |
| Kala | Yin sabuni da hannu | |
| Sunan aiki | Sabuni | |

Kayan hadī

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Asid soda litir 2 a 1000F kowane litar : 2000F |  | Soda kilo 2 a 2000F |
|  | Mai Dinor litir 9 a 5850F |  | Garin hilawa kilo 1 : 350F |
|  | Gishiri na 25 F |  | Bokiti 2 na ruwa a 10 F |
|  | Isansi mai kamshi butali 1 a 1000 F | | |
| Jimilla : 11.235 F CFA. | | | |

Kayan aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Bokiti babba na roba : 1.250 F |  | Babbar roba ta sa ruwa : 2.000 F |
|  | Mucciya : 500 F |  | Mululluka a: 10.000 F |
|  | Luddai na duma : 350 F |  | Safa ta hannu : 1.000 F |
| Jimilla : 15.100 F CFA | | | |



AGR 3

Yadda ake yin sabuni (kwana 2)

| Hotuna | Hayoyin | Bayani |
|---|---|---|
|  | A sa ma asid ruwa a bari ya yi awa 24 | |
|  | A sa litir 9 na mai Dinor (minti 2) | |
|  | A motsa har har sai ya yi kunu mai kabri (awa 2) | |
|  | A sa ma soda ASH ruwa a motsa (minti 10) | |
|  | Sa'annan a sa garin hilawa sai a riƙa motsawa sannu-sannu har ya zama tuwo (minti 30) | Kar a yi ma zare dauɗa |
|  | A sa isansi mai kamshin turare | |
|  | A sanya cikin mululluka | |

Yadda ake saidawa

| | | |
|---|---|---|
|  | Ana saidawa dunkule-dunƙule ko kuma kare-kare | A yi awo mai jan masaya. |

A yi tunani sosai tun kahin a soma sana'ar don a tabbata da in hidda uwa da ana samun riba.

Kuɗin kayan gami da sauransu : 11.235 F

Sabunin da aka yi : ɡuda 200 na wanka.

Lissahin riba bayan an saida:

Idan duka guda 200 aka saida:
150 F × 200 = 30.000 F
30.000 F – 11.235 F = 18.800 F
Ciniki - Uwa = Riba

In guda 74 aka saida:
11.200 F – 11.100 F = 100 F
Ciniki - Uwa = Riba kaɗan ce

Idan guda 80 aka saida, ana iya cin riba. Idan guda 70 aka saida
150 F x 70 F = 10.500 F
10.500 F – 11.200 F = - 700 F
Ciniki - Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba sai:

1. an yi lissahi da an tabbata tun farko da in a hidda duka abinda aka kashe da za a ci riba.
2. a dadaita yawan sabunin da za a yi da yawan masaya. Sabunin hannun na masu ƙaramin hali ne.
3. Yawanci masu mazamna unguyoyin talakkawa ne can ya kamata a kai sabunin a saida. Idan ana iya cin kasuwowi na ƙauye-ƙauye, ana iya samun ciniki.

A ƙarshe karatu na shekara, yan hutu yan lakkwal na yawan tahe-tahe suna iya sahen shi don su yi yan tahiya da shi.

4. Gargaɗi :

Asid da aka amfani da shi wajen yin sabuni abu ne mai kashewa a yi amfani da safa don kar ya taɓi jiki.
In an sa asid soda wani hayaƙi na tasowa, shaƙa shi na cuta ma ɗan adam, don haka a kiyaye da babu yara kusa.

Wannan irin sana'a akasari mata ke yin ta don biyan buƙatunsu da na iyalinsu da kuma taimakawa maras isasshen halin sayen sabuni na mashin mai tsada.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP02 |  |
| Sana'a | Sana'ar saida dambu | |
| Gari | Kalley ta kudu | |
| Kala | Sarrafa abinci da saidawa | |
| Sunan hausa | Yin dambu | |

Kayan hadī

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Buhu 1 na masara 15.000 F |  | Litir 5 na mai 3.250 F |
|  | Buhu 1 na tamakka 2.500 F |  | Tanka na 1.200 F |
|  | Tiya 2 na wake 1.200 F |  | Maji na 1.600 F |
|  | Kwanko 2 na digadige 1.800 F |  | ƙulli 2 na gishiri 100 F |
|  | Kanwa 25 F |  | Kan icce 2 500 F |
| Jimilla : 30.375 F CFA | | | |

Kayayyaki aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Tkunya 5 25.000 F |  | Koshiya ta 250 |

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Dozin 2 na koshiyoyi a 5.000 F |  | Babba koshiya ta miya a 1.000 F |
|  | Mayan kwanoni 2 a 14.000 F |  | Tukunyar sanholama 1 a 5.000 F |
|  | Faranti 35 a 3500 F |  | 4 plateaux à 4.000 F |
|  | Tiruruwa na ƙarhe 2 a 5.000 F |  | Mayan teburori a 15.000F |
|  | Banci 2 na katako a 12.000 F |  | Robobin sa ruwan sha a 14.000 F |
|  | Bokiti 2 na ƙarhe 3.000 F |  | Bokiti 2 na roba NA SA RUWA 3.000 F |
| Jimilla : 109.250 F | | | |
| | | | |
| | | | |

Ana dahuwa tun ƙarhe 3 zuwa ƙarhe 5 na sahe.

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | Tsintse ma masara ƙazamta (mintoci 15 zuwa 30) | Kar a bar ƙananan duwatsu. A zaɓi wake wanda ƙwari ba su taɓa ba |

| | | |
|---|---|---|
|  | A kai masara tahuna don a surhe ta | |
|  | A leɓaye masara (a hidda dussa) | |
|  | A kai masara bayan a leɓaye ta a tahuna don a yi tsaki | |
|  | A tankaɗe don a hidda gari | |
|  | A wanke tsakin da ruwa kaɗan | |
|  | A sa tsakin cikin tukunyar dambu | |
|  | A yi hiddowar farko don a motsa a sa ruwa | |
|  | A yi haka har sa 3, ga ta, ƙarshe sai a sanya mai da gishiri | |

Yadda ake saidawa

| | |
|---|---|
|  | Ana saidawa fala-fala cikin farantinnai |

A tabbata hidda uwa har riba ta shigo.

Kuɗin kayan aiki da sauransu (34.925 F CFA)
5.475 F
1.000 F = na kuɗin mota
300 F = na abinci

Yawan abincin da aka dafa
Dahuwa ta 40.200 F (fala 402 a 100F kowace fala)

Lissahin riba:
In an saida fala 402
402 Fcfa × 100 = 40.200 Fcfa
40200 Fcfa - 34.925 Fcfa = 5.275 Fcfa
Ciniki - Uwa = Riba

In fala 350 aka saida
100 Fcfa × 350 = 35.000 Fcfa
35.000 Fcfa - 34.925 Fcfa = 75 Fcfa Riba kaɗan ce
Ciniki - Uwa = Riba kaɗan ce sai an saida fala hiyye da 350.

In fala 300 aka saida
100 F × 300 = 30.000 F
30.000 F – 34.925 F = - 4925 F cfa
Ciniki - Uwa = Faɗuwa.

Idan ana son a ci riba

1. A lissafa da kyau tun farko sa saboda a tabbata da an hidda uwa riba na shigowa.
2. a sayi kayan dahuwa tun suna arha kamar kamar lokacin kaka (tiya 250F). Idan aka tattaro ƴan kuɗi sai a sayi cimaka mai yawa a adana.
3. a dafa abinci daidai da kasuwar da ake samu. Daga garuruwa mutane dayawa na tahowa yamai bayan sun ƙare ayukkan daji, akwai ciniki sosai ga damana babu ciniki ƙwarai saboda sun koma cikin ƙauye. A riƙa dahuwa tun da sassahe saboda masu sabkon hitowa da karin sahiyar yara.
4. a yi tunani su wanene ke sayan sana'ar. Tun da yara ke saya, a yi parashi mai sauƙi kamar 50F. A saida cikin lakkwaloli inda yara ke iya saye in sun hito shan iska.

Wannan sana'a, akasari mata ke yin ta don biyan buƙatunsu da na iyallansu. Wannan sana'a ba sai da kuɗi mai yawa ake yin ta kuma tana rage ma mata dogara ƙwarai ga maza wajan biyan buƙatun wasu kashe-kashe.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP03 |  |
| Sana'a | ƙera takalma balka | |
| Gari | Gidan artizana wadata | |
| Kala | Sarrafa fata don a yi takalma balka da saidawa | |
| Sunan hausa | ƙera balka | |

ilalan

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | ƙirgin shanu : 11000F |  | Kwal : 100F |
|  | ƙirgin shanu : 1750F |  | Mai : 50F |
|  | Metir 4 na zare : 200F |  | yan bito 5 : 125F |
|  | Garura : 1300F |  | ƙananan ƙusoshi 10 : 100F |
| Jimilla : 14.625F CFA | | | |

Kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Almakashi 3 : 3000F |  | magargari :1250F |
|  | Yuƙa 1 :1500F |  | Marto 1 :2500F |
|  | ƙusa (talan) :500F |  | Wasu ƙaruffa 3 dabam-dabam (istop) :2900F |

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Icce (albu) :2000F |  | koshigi :5000F |
| Jimilla : 18650 F CFA | | | |

Ciniki

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A aikata fata da magargari da albu awa 3 | A hidda duka gasussuka |
|  | A yanka fata, a sa mata mai don ta yi haske da taushi (awa1) | |
|  | A yi kamanun irin takalma a ɗumke (minti 30) | A auna takin takalma da kyau |
|  | A sa irin garurar da ake so (minti 30) | |
|  | A hauda takalma (awa 1) | |
|  | A ɗumke a buga ƙusa a yi ado da ƙusar ado | |

Yadda ake saidawa

| | |
|---|---|
|  | Taki guda-guda |

A yi tunani tun kahin a soma sana'ar don a tabbatar da bayan an hidda uwa riba na iya shigowa mai kabri.

Kuɗin kayan haɗi
14625F cfa
400 F kuɗin takis
1000F na abinci
Jimilla : 16025F

Quantité de production
5 paires de balka à 6250F'B5= 31250F

Lissahin riba ta in saida balka 5
In an saida duka
31250cfa -16O25 F cfa =15225F
Ciniki - Uwa = Riba

In an saida taki 2
625O cfa × 2 = 125OOF cfa
12500 F cfa - 16O25F cfa = -3525 F kenan sai an saida hiye da haka

In an saida taki 3
6250 F cfa × 3 = 18750F cfa
18750F cfa - 16025 Fcfa = 2.725F cfa
Ciniki - Uwa = Riba

Idan ana son cin riba :

1. a yi lissahin da zai bada dama ta gano tabbat akwai riba tun kahin a shiga sana'ar.
2. a sayi kaya gami tun suna arha.
3. a zan yin takalman daidai da kasuwar da ake samu. Kuma a zan yin na kirki.
4. a riƙa amfani da salloli da kuma kasuwar duniya don a saida dayawa.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP04 |  |
| Sana'a | Umkin darori | |
| Gari | Karamar hukuma yamai 3 | |
| Kala | Umkin darori | |
| Sunan hausa | Umkin darori | |

Kayayyaki (suna, yawa, parashi da sauransu)

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Tisi metir 12 a 600F |  | Allura ta 25 F |
|  | Zaren ɗumki darori guda 12 : 3.000F |  | ƙaramin zare na 75 : 225F |
|  | Zare na buroe na mashin | | |
| Jimilla : 10.875 F CFA. | | | |

Kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Metir na awo 250F |  | Takardar dekalki 100F |
|  | Ja-layi (regil) :150 F |  | Karanyo da magogi : 250F |
|  | Hoto : 100 F |  | Almakashi : 500 F |
|  | Mashin (tela) 200.000 F |  | Mashin (tela) ƙarama 70.000 F |

Yadda ake ɗumka darori

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A auna tisi, a yanka don hudda dara da matassai (minti 30) | A yi amfani da babba tebur |
|  | A ɗumka burode na dara da matassai (minti 30) | A ɗumke dara da matassai da kyau. |
|  | A yi dekalkin hotuna (desin) bisa dara da matassai | Kar a yi tisu dauɗa |
|  | A yi buroden tisu (kwana 3) | A yi aiki da zaren da ya hi dacewa (launi) |
|  | Ana iya yin buroden da tela | A yi aiki da zaren ya hi dacewa. |

Yadda ake saidawa

| | | |
|---|---|---|
|  | A sa cikin leda | A goge dara da matassai da kyau |

A yi tunani kahin a soma sana'ar don a tabbata da lalle za a hiddo uwa har a sami riba.

Kuɗin kaya
Tisu (metir 12) a 7600F
Zaren burode a 3200F
Zare ƙarami a 75F
Allura a 25F
kuɗin mota a 800F
jimilla : 11.700F

yawan darorin da aka yi
dara 1 duka kwana 15 kenan darori 2 a wata

idan ana iya saida darori a wata a 20.000F kowace dara
40.000 F – 23.400 F = 16.600 F CFA na riba a kwatamce 500 kowace rana.

In dara 1 aka iya saidawa
20.000 Fcfa – 11.700 F = 8.300 F a wata, 275 F CFA kowace rana, sun yi kaɗan har a aje wani abu.

Idan ana son cin riba

1. a yi nazari don farko a san tabbat za a ci riba.
2. a sayi kayan da ya kamata tun suna da arha ba sai kusan salloli ba.
   Kuɗin zare da na tisi na canzawa har ma in salloli suka yo kusa. Metir 1 na iya kai 600F har 800F. In an haɗa kuɗi kaɗan sai a sayi kayayyaki a adana.
3. a yi aiki da buƙatar mutane masu son darori, ana iya ɗumka darori kamar 30 a shekara a kwatamce darori 2 zuwa 3 a wata.
4. a yi nazari bisa ga wasu dubaru na saidawa. In ana bukukuwa, ana iya gwadin darorin da aka ɗumka don mafi yawan saye a non ake samunsu.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP05 |  |
| Sana'a | Tuyar fanke | |
| Gari | Kasuwar bonkanai | |
| Kala | Sarrafar abinci da saidawa | |
| Sunan hausa | Fanke | |

Abubuwan hadī ( suna、yawan、parashi da sauransu)

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Garin fari kilo 1500F |  | An maji 3 mai zakara 175F |
|  | ƙulli 1 na tanka 100F |  | Koshiya 2 na tumati ta kwanko 50F |
|  | Kuli kanwa 25F |  | ƙulli gishiri 25F |
|  | An albasa 1 50F |  | Litir 2 da rabi 1.565F |
|  | ƙullin sukari 1 na 150F |  | Farmanganati 100F |
|  | Kan icce 2 na 200F | | |
| Jimilla : 3.940 F CFA. | | | |

Kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Kasko 700 F |  | Babban kwano 6.000 F |
|  | Koshiya tsame : 125 F |  | Koshiyyai : 175 F |

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Luddai 1 na 125 F |  | Faranti babba a 2.500 F |
|  | Murhu na 350 F |  | Kwano babba na 2.000 F |
| Jimilla : 11.975 F CFA | | | |

Yadda ake tuya biskiti

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A tankaɗe gari fari (munti 15) | |
|  | A sa dalabu cikin ruwa masu damar zahi, a zuba cikin gari, sai a kwaɓa | |
|  | A sa dan gishiri, kanwa da sukari cikin garin a ci gaba da kwabawa | |
|  | A bar garin har ya taso | Don a hana garin ya bushe a zuba mai saman garin |
|  | A kwaɓa kuma ana sa ruwa kaɗan-kaɗan sai ana ɗebowa kaɗan-kaɗan. | Ana sa wa cikin mai |
|  | Karshe tuya | A sa cikin babban daro mai tsabta |
|  | Miya: A dafa tanka attarugu, kankatsatsar albasa, maji, tumati, gishiri da mai sai a sanya ruwa ya zama miya. | Ana cin shi kuma da sukari |

Yadda ake saidawa (misali)

| | | |
|---|---|---|
|  | Ana saida a cikin ledodi | |
|  | Ana sa cikin burodi a yi "silansiye" | Wasu suna buƙatar a zuba musu ɗan mai bayan miya |
|  | Ana saida cikin farantinnai. | |

A yi tunani kahin a fara sana'ar don a tabbata da in an hidda uwa riba na iya shigowa.

Kuɗin kayan gami: 3.940 F

Fanken da aka yi :
5 Fcfa × 1000 = 5.000 Fcfa
Ciniki – Uwa = Rba

In guda 788 aka saida
5 Fcfa × 788 = 3.940 Fcfa
3.940 Fcfa - 3.940 Fcfa = 0Fcfa
Ciniki – Uwa = ba Rba, ba faɗuwa
Don haka sai an saida hiye da haka

In guda 250 ne aka saida
5 Fcfa × 250 = 2.500 Fcfa
2.500 Fcfa - 3.940 Fcfa = - 1.440 Fcfa
Ciniki – Uwa = faɗuwa

Don a ci riba sai an yi aiki da gargaɗi kamar haka :

1. a yi nazari tun kahin a shiga sana'a don a san uwa har a ci riba.
2. a yi fanken daidai da yawan masaya. A cikin garuruwan karkara, mutane dayawa cin rani suke zuwa. Ba a samu ciniki ƙwarai, idan aka toya da yawa ana iya yin kwantai sai a yi faɗuwa.
3. a yi tunani su wanene masaya? In yara ne ke saye, a yi parashi daidai da ƙarhin yara.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP06 |  |
| Sana'a | ƙira ta fata | |
| Gari | Yamai gidan artisana na wadata | |
| Kala | ƙera kayayyaki da fata | |
| Sunan hausa | Aikin fata (ƙira ta fata) | |

Kayayyakin gami

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | ƙirgin shanu 11.000 F CFA |  | Fatar akuya 1.750 F |
|  | Tuwo masara 50 F |  | Garura 1.300 F |
|  | Zare metir 4 na 200 F |  | Fatar maciji 5.000 F |
|  | Mai Dinor ko na gujjiya na 50 F |  | ƙusoshi kala-kala 225 F |
| Jimilla : 19.575 F CFA. | | | |

Kayan aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Almakashi 3.000 F |  | Yuƙa 1.500 F |
|  | Allura 250 F |  | Manyan ƙusa 500 F |
|  | Icce (albu) 2.000 F. |  | Karhe (koshigi) 5.000 F |

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Magargari 1.250 F |  | marto 2.500 F |
|  | Ƙarhe kala (istop) : 3 750 + 150 + 2.000 = 2.900 F | | |
| Jimilla : 18.900 FCFA | | | |

Yadda ake yin takalmi

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A aikata fata da albu da magargari tsawon awawi 3 | A hidda gasussuka |
|  | A yayyanke fata sai anan a sa mai don ta yi haske da taushi awa 1 | |
|  | A hidda kamanun takalma (talon) sa'anan a ɗumke da hannu | A daidaita takin don girmansu ya zo daidai |
|  | A sanya ma fatar akuwa garura wadda aka yanka (minti 15) | |
|  | A hauda takalman (awa 1) | |

Yadda aka saidawa

| | | |
|---|---|---|
|  | Cikin leda aka saidawa | |

A yi nazari don a tabbata da lalle za a ci riba in an hidda uwa kahin a fara sana'a.

Kuɗin kayan gami :
19.575 F CFA
Yawan takalman da aka yi :
Takin takalma 5 « balka »
Takin takalma 3 « fanka »
Takin takalma 4 « na shakane »

Lissahin riba :
In an saida taki 12 duka :
2.500 F × 5 = 12.500 F
3.500 F x 3 = 10.500 F
2.750 F x 4 = 11.000 F
Jimilla : 34 000F
34.000F – 19.575 F = 14.425 F
Ciniki – Uwa = Rba

In taki 7 ne aka saida
2.500 F × 3 = 7.500 F
3.500 F x 1 = 3.500 F
2.750 F x 3 = 8.250 F
Jimilla : 19.250F
19.575 F – 19.250 F = 325 F
Ciniki – Uwa = Rba kaɗen ce kenan sai an saida hiye da taki 7

In taki 6 aka saida:
2.500 F × 2 = 5.000 F
3.500 F x 2 = 7.000 F
2.750 F x 2 = 5.500 F
Jimilla : 17.500 F,
17.500 F – 19.575 F = - 2.075 F
Ciniki – Uwa = Faɗuwa

Idan ana son ci riba to sai:

1. an yi nazari a kwatamce a gani tabbat riba na iya shigowa bayan an hidda uwa.
2. a yi takalma daidai yawan masaya don kar a samu rishin ciniki.
3. a yi tunani don a gano masu saye.

Kayan ƙira ta hannu kaya ne da turawa yan yawan buɗe ido ke buƙata ƙwarai. Mafi yawan kayan suke sanyo su don haka a riƙa talla a wuraren da suke sabka ko suke zuwa a kai a kai har lokacin zakkuwasu.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP07 |  |
| Sana'a | Saƙa sakala | |
| Gari | Gidan kallo na yamai | |
| Kala | Saƙa sakala (aikin hannu) | |
| Sunan hausa | Saƙa sakala | |

Kayayyakin gami

| | |
|---|---|
|  | Fake 4 na zare dabam-dabam : 16000F<br>yan itace 8 = 800F<br>Kala 3 na garura : 3.000F |
| Jimilla : 19.800F | |

kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Runfa zaman saƙa : 5.000F<br>Abin saƙa 5 : 2.500F<br>Abin takawa 2 : 200F | | Kujera ta icce : 3.000F<br>Tabarma : 600F |
|  | Abin juyawa da abin ja aɗaure : 1500F<br>Dutsi 1 | | |
| Jimilla : 12.800F | | | |

yadda ake saƙa sakala

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | Saƙar saƙa a na ta cikin na'urar saƙa : awa 2 da rabi | |
|  | A naɗa zare (awa 2) | |
|  | A fara saƙa bandodi 7 zuwa 15 : awa 1 zuwa 3 | |
|  | A saƙa zare cikin sati 2 | Kar a bari zare ya yi dauɗa |

Yadda ake saidawa

| | |
|---|---|
|  | Ana saida sakala gudaguda a 30.000F ko hiye da haka amma hawa-hawa ce. |

A tabbatat a kwatamce da in an hidda uwa riba na shigowa tun kahin a fara sana'ar.

Kayan gami da sauransu :

19800F
400 F na mota
Jimilla : 20200F

Yawan sakkalun da aka saƙa : sakala 1

Lissahin riba :
In an saida sakala 1 a 30.000F
30000 F × 1 = 3000 F
30.000 F – 20200F = 9800 F a cikin kwana 14 700F kowace rana.
Ciniki – Uwa = Riba

In sakala 1 aka saida a cikin wata 3
30000F – 20200=9800F a cikin kwana 90 = 108F kowace rana
jours soit 108 F par jour
Ciniki – Uwa = Riba kaɗan

In a cikin wata 2 ne za a sami riba 163 kowace rana .
30.000 F – 20.200 F = 9800 F a cikin kwana 120 :13F na riba rana 1
Ciniki – Uwa = ba Riba ba uwa ba sami komi ba.

Idan ana son cin riba :

1. a kwatamta tun daga farko don a san tabbat riba za ta shigo.
2. a yo cinikin ƙwarai na zaruruwa (arha) masu kyau.
   kuɗi dabam-dabam daga ƴan kasuwa ne (ƙulli zare na tashi 3.500F zuwa 4.000F)
3. yawan sakalolin da za a saƙa ya zan daidai da yawan masu so. waɗannan irin kaya mutane ne ke cewa a saƙa masu. A rage ranakku saƙa a maido su kwana 10 kambacin kwana 14.
4. a yi tunani don a san su wanene masaya. Mafi yawa amare ne ke sayen sakallu. Sai ana yi ana talla lokacin bukukuwa.

Wannan sana'a na taimakawa wajen biya ma iyali buƙatu ko da yake sai an sami mai so ne aka saƙewa don in ba haka akwai saidawa.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP08 |  |
| Sana'a | Saida mayan kujeru (salon) | |
| Gari | Yamai ƙaramar hukuma ta 3 | |
| Kala | Kahinta da saida mayan kujeru (salon) | |
| Sunan hausa | Kahinta da saida salon | |

Kayan gami

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Kwanhile 1 na kadir kin mayan kujeru 80.000F |  | Sifon na katifa 30.000 F |
|  | Tisi metir 30 30.000 F |  | ƙulli kaushu 1.500 F |
|  | Buhuna 15 yamti 1.875 F |  | Kwal 1.500 F |
|  | Zare na 1.250 F |  | Kartuna yamti 2.500 F |
|  | Kilo 3 na ƙusa 3.000 F | | |
| Jimilla : 151.625 F CFA | | | |

Kayayyaki aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Rabo 2.000 F |  | Marto 3 a 4.500 F |
|  | Sentimetir 250 F |  | Tenayi abin cire ƙusa 2.000 F |

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Tornivis pausi yuƙa da lim 5000F |  | Babban tebur 15.000 F |
|  | cilmidas 1 a 500 F | | |
| Jimilla : 29.250 F CFA | | | |

Yadda ake yin salon

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A yi kadirori shanta (awa 2). | |
|  | A auna a yanka tisi da shifou (awa 1) | |
|  | A hauda kaushu wajen matassan kai da wurin bai (awa 1) | A hidda wata ƙasa da ke can ciki |
|  | A hauda buhuna | |
|  | A hauda shifon (minti 30) | |
|  | A ɗumke tisi da aka yanka a daidaita shi da kamanun salon (minti 30) | |
|  | A hauda tisi (awa 1 da rabi) | |

Yadda aka saidawa

|  | Ana saida salon kwanhile (kujera babba mai wuri 3 da kujeru 4 masu wuri guda-guda. |
|---|---|

A yi tunani daga farko, a kwatamta a gani lalle ana iya cin riba bayan an hidda uwa.

Kuɗin kaya :
151.625 F
3.000 F na kuɗin mota
50.000 F biyan ƴan aiki
Jimilla : 204.625 F CFA

Yawan kayan da aka yi :
Salon 1 (dogo 1, da 4 ƙanana)

Lissahin riba
In an saida salon 1 duka :
500.000 F × 1 = 500.000 F
500.000 F – 204.625 F = 295.375 F
Ciniki – Uwa = Riba

In za a saida da gaugawa kuɗin ragewa zai yi:
200.000 F × 1 = 200.000 F
204.625 F – 200.000 Fcfa = - 4.625 F
Ciniki – Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba:

1. a yi lissahin da za sami riba ko da a kwatamce ne.
2. a ƙera salon-salon daidai da buƙatar salon kamar amare da ƴan bariki matasa. Akwai masaya lalle amma kar a yi dayawa a shiga jira masu saye. A yi aiki da sai mutun ya ce yana so a yi mishi.

A kusan salloli mutane na son canza rigar salon ko salon kin gabaɗaya. Sana'a ce da maza ne ke yin ta kuma tana son jari mai yawa da sanin aiki (iyawa). Da wannan sana'a ana iya biya ma iyali buƙatu har a aje wani abu.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP09 |  |
| Sana'a | Yin mai na gujjiya | |
| Gari | Kasuwar bonkanay | |
| Kala | Sarrafa kayan gona | |
| Sunan hausa | Hidda mai na gujjiya | |

Kayan gami ( suna、yawa、parashi da sauransu )

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Tiya 6 na tsabar gujjiya 5.000F |  | ƙulli 2 na gishiri |
|  | Kan icce 1 na ƙuna 500F |  | Ruwa na 15F |
| Jimilla : 5.515 F CFA | | | |

Kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Daro 1 na sa ruwa = 400 F |  | ƙaramar tasa da ake aza tasa hudodi kan ta 350F |
|  | Babbar kwarya 3 da ƙarama 1 a 250 F + 1.500 F= 1.750 F |  | Robobi 2 na 6000F |
|  | Kasko na 1.500 F |  | Mulu na tiya 6 a 600F |
|  | Koshiya ta 100 F |  | Luddai 1 a 250 F |
|  | Kwano mai hudodi kasa 600 F |  | Faranti (tire) na 1.000 F |

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Mataci = 500 F |  | Murhu a 1.000 F |
|  | Turmi 1 =5.500 F |  | An katako ko dutsi a 150F |
|  | Tabarma 1 = 1.000 F |  | Tame a 500 F |

Yin mai (na ɗankai kwana 2)

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | Tsintse ƴan duwatsu da ke cikin gujjiya (minti 90) | |
|  | A ba rairai da ke cikin kasko wuta (minti 10) | A yi aiki da rairai fari maras duwatsu |
|  | A sa gujjiya cikin rairai don a soye ta (minti 60) | Faire cela petit à petit jusqu'à épuiser la quantité d'arachide. |
|  | A motsa daɗan-kaɗan kar a tsaya sai ta sayu | A sa wuta maras ƙarhi |
|  | A hidda gujjiya | A yi amfani in son samu da ƙwarya |

| | | |
|---|---|---|
|  | A hidda gujjiya daga cikin ƙasa (minti 60) | A yi amfani da tame |
|  | A shanya gujjiya kan tabarma | A yi amfani da tabarma son samu |
|  | Da ɗan ƙaramin katako a motsa gujjiya don ƙwalfa ta hidda | A yi hankali kar a farfashe gujjiya |
|  | A zuba cikin ƙwarya | |
|  | A sheƙe ƙwalfa don a sami ɗiyan gujjiya kaɗai (minti 120) | Kar a bar ma gujjiya ƙwalfa dayawa |
|  | waɗannan ɗiyan gujjiya farare su ake niƙewa da dutsi ko mashin (minti 2) | A niƙe da kyau |
|  | Dawon gujjiya bayan a hito daga mashin (minti 10) | |
|  | A sa dawo cikin turmi | Kar a yi sake ƙasa ta shiga cikin turmi. In dawo na da yawa a raba |
|  | A sanya ruwa kaɗan | A yi amfani da ruwan zahi |

| | | |
|---|---|---|
|  | A saɓa dawon da taɓarya | Sai an ɗauki hanƙuri da kuzari |
|  | A motsa dawon da taɓarya da ke cikin turmi kar dawon ya yi launi ɗaya. | |
|  | Dawon sai ya ɗauki launin ja-ja | |
|  | Mai na fara hita kaɗan-kaɗan | |
|  | A sa luddai ana ɗebo mai (awa 4) | |
|  | A sa mai cikin yar babbar tasa | |
|  | A hiddo sauran dawo a sa cikin roba | |
|  | A yi mulamulai ƙuli-ƙuli da dawon (awa 2) | |
|  | A zuba mai cikin kaskon da ke saman wuta. | |

| | | |
|---|---|---|
|  | A sa mulamulan ƙuli-ƙuli cikin mai | |
|  | A motsa mulamulan | |
|  | Za a sami a ƙalla ɗan ƙuli-ƙuli 1500 (awa 2) | |
|  | Idan mai ya soyu da kyau sai a yi dahuwa da shi ana samun litir 2,5 | |

Yadda ake saidawa

| | | |
|---|---|---|
|  | Ana saidawa liti-litir a 750F | Mutane sun hi son mai na gujjiya da duk wani mai har ma in za a yi yamutse |
|  | Ana saida ƙuli-ƙuli biya dala | |

A yi tunani don a tabbata da lalle in an hidda uwa riba tana shigowa tun farko.

Kuɗin kayan gami : 6.1901F
Tiya 6/800 F/ tiya = 4.800 F
Bokiti 1 = 15 F
Gishiri = 75 F CFA
Itace = 500 F CFA
kuɗin mota = 200 F
kuɗin niƙa = 600 F

yawan mai da aka yi :
litir 6 da ƙuli-ƙuli 1500

lissahin riba

in an saida litir a 750, ƙuli-ƙuli 2 dala
750 F × 6 = 4.500F
5 F x (1.500 /2) = 3.750 F
8.250 F - 6.190 F = 2.060 F
Ciniki – Uwa = Riba

In litir 4 kawai aka hiddo da ƙuli-ƙuli 1500
750 F/litir ×4 litire = 3.000 F et 3.750 F ƙuli-ƙuli = 6.750 F
6.750 F – 6.190 F = 560 F
Ciniki – Uwa = Riba kaɗan ce
Ba za a ci riba sosai sai an hidda hiye da litir 5 da ƙuli-ƙuli guda 1500. lokacin hidda yahi wuya don haka kala dawon na ƙarhi kala mai na ragewa.

In litir 3 ne aka hiddo
750 Fcfa × 3 = 2.250 Fcfa et 3.750 F = 6.000 F CFA,
6.000 Fcfa – 6.190 Fcfa = - 190 F
Ciniki – Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba

1. a lissahin tabbata riba ko da a misalce ne.
2. a sayi kayan gami tun ba su yi tsada ba. kuɗin gujjiya na sakewa (tiya 800F zuwa 1600F).
   A samo kuɗi a saye ga kaka a aje.
3. a kayyade daidai yawan mai wanda ake iya yi dangance da lokacin ake da dama.

Sana'a ce da mata ke yi waɗanda ke zaune a cikin karkara da ake noma gujjiya. Wannan sana'a na tallaba ma iyali wajen biya musu buƙatunsu.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP10 |  |
| Sana'a | Sana'a kayan zinariya da azurfa | |
| Gari | Gidan artizana wadata yamai | |
| Kala | Aikin hannu | |
| Sunan hausa | Saida zinariya da azurfa | |

Kuɗin sayen kayan da aka ƙéra (suna, yawan , parashi da sauransu)

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Dan warwaro 15 = 300.000 F |  | Zobe 100 = 200.000 F |
|  | Sarƙa 30 = 450000F |  | yan kunnai 300 = 300.000 F |
|  | Kurwa 50 = 300.000 F | | |
| Jimilla : 1.550.000 F | | | |

Kayan aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | 5 Pinces : 6.000 F |  | 1 Enclume à 2.000 F |
|  | 12 Lûmes à 11.500 F |  | 3 Ciseaux à 4.000 F |
|  | 1 soufflet à 20.000 F |  | Pointe à graphe 2.000 F |

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Buros 1 na ƙarhe = 1.500 F |  | Shalimo = 15.000F |
|  | Marto 3 = 15.000 F |  | Zartu 2 = 12.000 F |

Yadda ake ƙera kaya

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A auna azurfa garam 15 a narke ta (minti 20). | A yi hankali in babu ƙasa cikin tukunya |
|  | A kara burakis a cikin narkakkar azurfa (minti 10) | |
|  | A zuba narkakkar azurfa a cikin mlu mai bada kama (minti 5) | |
|  | A aikata abinda aka ƙera har ya yi daidai da yadda ake sa (minti 15) | |
|  | A yi yadda zai ɗciki kamar dunkule sai ayi suden bakunan 2 (minti 5) | |
|  | A zoze kuma a yi zoben ado uma a wanke da ruwan zahi tare da sa ɗan gishiri (minti 10) | |

Kuɗin sayen kayan aiki

| | |
|---|---|
|  | Azurfa : 900.000 F |
| Jimilla | 900.000 F |

Yadda ake saidawa

| | |
|---|---|
|  | Guda-guda ko taki na biyu-biyu in ƴan kunnai ne |

A yi lissahi don a tabbata tun daga farko ko da a yi misali ne da in an hidda uwa ana iya cin riba.

Kuɗin sayen kaya : 900.000 F

Kuɗin saidawa : 1.550.000 F

Lissahin riba :
In an saida duk
1550000F – 900000F = 650.000F.
Ciniki – Uwa = Riba

In rabi ne aka saida :
775.000 F – 90.000 F= - 125000 F
Ciniki – Uwa = Faɗuwa
Kenan sai an saida hiye da rabi

Idan ana son cin riba

1. a lissahi don a tabbata da lalle in an hidda uwa riba za ta shigo.
2. a yi nazari su wanene masu saye.
3. a saida lokacin kasuwar baza koli ko salloli.
4. a yi ƙira mai kyau.

Sana'a ce da maza ke yin ta kuma bugaje kuma gadonta aka yi. Ana iya biya ma iyali buƙatunsu da wannan irin sana'a ko da yake ba kowa ke yin wannan sana'a saboda a dauke sana'ar mutane ƴan ƙananan gida.

Kundi sana'o'i : Masu yin kaya (sarrafawa)

| | |
|---|---|
| Lamba | NP11 |
| Sana'a | Rini |
| Gari | Gidan kallo na yamai |
| Kala | Aikin hannu |
| Sunan hausa | Rini |



Kayan gami

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Tisi wanda ba yada ado na kaɗa 100/100 metir 2,5 = 1.500F |  | Buji pahe 1 = 350F |
|  | Garura = 1.500 F |  | Sudu = 2000F |
|  | Kalanzir = 500F |  | Ruwa = 15 F |
|  | Itace = 100F |  | Gawai = 125F |
| Jimilla : 6.090 F CFA. | | | |

Kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Panso 2 =900F |  | Murhu (manjamar) = 350F |
|  | Dutsi guga = 3000F |  | Kwanko yamti = 100F |
|  | Roba 1 = 2.500F |  | Bokiti 1 = 1.500F |

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Bokiti yamti na fantir = 500F |  | Tebur = 10.000F |
|  | Tano na ƙarhe = 2000F |  | Kujera : 3.500F |
|  | Bik, karayyo, gwam, dan zane = 115F | | |
| Jimilla : 24.465 F | | | |

Yadda ake rini

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A zaɓi zane mai kyau sai a zana bisa tisi (awa 1) | |
|  | A narke buji a cikin kwano yamti da ke saman murhu (minti 5) | |
|  | A sa panso cikin ruwan buji ana shafawa kan zanen da aka yi bisa tisi (awa 3) | A yi hankali a bi zanen sau da ƙafa |
|  | A rhe can ciki da buji (awa 1) | |
|  | A shirya garura (minti 15) | |
|  | A jika tisi cikin garura (minti 20) | |

| | | |
|---|---|---|
|  | A shanya tisin da aka rini ya bushe | A barshi ya bushe kuma ana yi ana jan tisi har kamarshi ta hita. |
|  | A hidda buji da yuƙa sa'anan a sake wanke tisin (awa 1) | |
|  | Sa anan sai wanke da kalanzir mai zahi (minti 30) | |
|  | A goge tisi bayan ya bushe (minti 10) | |

Yadda ake saidawa

| | | |
|---|---|---|
|  | Tabulo-tabulo ake saidawa kala 5 tabulo-tabulo yake. | |

A yi lissahi tun farko kahin a fara sana'a don a tabbata ko da a misalce ne da in an hidda uwa riba na hitowa.

Kuɗin kayan gami :
6.090 F
1.000F F na zuba – zuba na gidan kallo
400 F kuɗin takasi
500 F na abincin ini
Jimilla : 7.990 F CFA

Yawan aikin da aka yi :
Tabulo 5 madaidaita

Lissahin riba bayan an saida
In an saida duka:
3.000 F × 5 = 15.000 F
15.000 F – 7.990 F = 7.010 F
Ciniki – Uwa = Riba

In an saida guda 3
9.000 F – 7.990 F = 1 .010 F
Ciniki – Uwa = Riba kaɗan ce

In an saida guda 2 kawai
3.000 F x 2 F = 6.000 F
6.000 F – 7.990 F = - 1.990 F
Ciniki – Uwa = Faɗuwa

**Idan ana son cin riba:**

1. a lissahi tun farko don tabbatat lalle riba za ta samuwa.
2. a yi rini mai kyau tare da aiki da launi mai kyau.
3. a rina daidai da buƙatar masu saye. Kayan rini na da ruwan kasuwa ga baƙi ƴan yawon buɗe ido.
4. Gargaɗi: a yi hankali da hasken rana saboda yana ɓata launi kaya.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP11 |  |
| Sana'a | Bombo galase | |
| Gari | Unguwar kallai ta kudu | |
| Kala | Sarrafa kaya da saidawa | |
| Sunan hausa | Bombo galase | |

Kayan gami (suna、yawa、parashi. )

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Garin ɗiyan kuka kilo 1,5 = 300F |  | Aromatik = 350 F |
|  | Kilo 2 na sukari = |  | Kunnuwa masu ƙamshin anana = 50F |
|  | Ruwa = 10 F |  | Garura = 100 F |
| Jimilla : 1.810 F CFA. | | | |

Kayan aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Firigo = 300.000 F |  | Tame = 250 F |
|  | Bokiti 2 = 2.500 F |  | Tarmos 2 =: 25.000 F |
|  | Luddai = 125 F | | Wutar lantarki : 15.000 F /wata |
| Jimilla : 327.875 F CFA | | | |

Yadda ake yi bombo galase

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A tankaɗe garin ɗiyan kuka (minti 15) | A sa sukari da aromatik da ruwa masu ƙamshi |
|  | A sa ma garin ruwa (minti 10) | a motsa duka haɗin (minti 5) |
|  | A motsa da luddai (minti 30) | A yi amfani da luddai don sa a cikin lrdodi (minti 60) |
|  | A ƙulla cikin ledodi | A sa cikin firigo |
|  | | In su zamma galas sai a saida |

Yadda ake saidawa

| | |
|---|---|
|  | ƙulli-ƙulli na ledodi |

A yi tunani kahin a fara sana'a dan a tabbata da za a sami riba.

Kuɗin kayan gami

1.810 F
Paken leda 5 : 750 F
KuƊin wuta : 500 F ini
Jimilla : 3.060 F

Yawan bombo galase
Bomobo guda 200 : 5.000 F

Lissahin riba :

In an saida guda 200
25 F × 200 = 5.000 F
5.000 F – 3.060 F = 1.940 F
Cinik – Uwa = Riba

In guda 92 aka saida
25 F × 92 = 2.300 F
2.300 F – 3.060 F = - 760 F
Cinik – Uwa = Faɗuwa
Kenan sai an saida hiye da haka in ana son cin riba.

Idan ana son cin riba

1. sai an yi lissahi an tabbata lalle riba tana shigowa ko daa kwatamce ne.
2. a yi bombo galase daidai da buƙatar kasuwa.
3. a yi tunani don a san su wanene masaya. In yara ne a yi parashi mai sauƙi. Kar a yi shi ga lokacin ɗari.
4. a yi bombo na dala-dala don yara su zo su saye.

Sana'a a ce wadda mata ne ke yinta kuma tana son jalli mai kabri da kuma wutar lantarki da firigo.
Da wannan sana'a ana iya biya iyali wasu buƙatu kamar sayen kayan lakkwal, abinci, tufaya da sauransu.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP12 |  |
| Sana'a | Sana'a saida kafa (tuwon masara) | |
| Gari | Kasuwar bonkanai | |
| Kala | Sana'a sarrafa abinci da saidawa | |
| Sunan hausa | Sana'a saida kafa (tuwon masara) | |

Kayan gami

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Rabin (1/2) buhun masara = 7.500 F |  | ƙulli kola 2 = 500 F |
|  | Itace ƙuna = 300 F |  | Ruwa = 100 F |
| Jimilla : 8.400 F CFA | | | |

Kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Tukunya 1 = 10.000 F |  | Koshiya ƙarama = 250 F |
|  | Ispatil 1 = 500 F |  | Luddai 2 = 500 F |
|  | Babban murhu = 1000 F |  | Bokiti 2 = 2.000 F |
|  | Robobin sa ruwa = 3.800 F |  | Tukunyar laka 2 = 2.500 F |
|  | Tabarmi 2 = 1.000 F |  | Tame 2 = 1.000 F |
|  | Faranti = 1.500 F |  | ƙwarya 2 = 1.000 F |
| Jimilla 24.800 F | | | |

Yadda ake yin kafa

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A hidda ma masara ƙazamta, a hidda dusa bayan an surhe (minti 30-45). | Kar a bar ɗan tsakuwa ko guda. |
|  | A sa masara tsari tsawon kwana 2 | |
|  | A ƙashire da kyan, a shanya kan tabarmi (minti 15) | A yi hankali da ƙura |
|  | A yi garin masara (ɗakawa ko mashin) | |
|  | A zuba garin masara cikin roba mai ruwa. A motsa da luddai (minti 10) | A yi hankali da ƙwari ko wata ƙazamta |
|  | A yi amfani da mataci na tisi don hidda tsaki (minti 20) | |
|  | Hurar da aka samu a sa ta a tukunya a ba ta wuta, ba a motsawa a ɗeba ruwa a bar dawon (minti 20) | A yi hankali da ƙwari da ƙazamta |
|  | A ƙuna wuta a aza tukunya cike da ruwa | |
|  | A ɗebo dawo-dawon ƙadan-ƙadan, ana yi ana motsawa da ispatil har ta yi ƙarhi (awo 1) | A yi hankali da ƙwari da ƙazamta |

| | | |
|---|---|---|
|  | Da luddai sai ana ɗebowa ana sawa ga leɗodi (luddai 2 kowace leda) ana ƙullewa. | A wanke hannuwa da kyau kahin a soma |

Yadda ake saidawa

| | |
|---|---|
|  | Ana saida kafa ƙulli-ƙulli cikin leda. |

A yi tunani tun farko don a tabbata da lalle za a sami riba bayan an hidda uwa.
**Kuɗin kayan gami (8.800 F)**
8.400 F
400 F = kuɗin mota takasi
Yawan kafar da aka ƙulla
Yi guda = 15.000 F (ƙulli 600 X 25 F)

**Lissahi riba bayan saida wa**
In an saida ƙulli 600
25 F × 600 = 15.000 F
15.000 F - 8.800 F = 6.200 F
Ciniki – uwa = riba

In guda 352 aka saida =
25 F × 352 = 8.800 F
8.800 F - 8.800 F = 0 F
Ciniki – uwa = ba riba, ba faɗuwa

In guda 300 aka saida
25 F × 300 = 7.500 F
7.500 F – 8.800 F = - 1.300 F
Ciniki – uwa = faɗuwa

**Don idan ana son cin riba :**

1. A yi nazari yadda riba za ta shigo tun farko ko da a kwatamce ne.
2. A sayi kayan gami tun suna da arha. Ga kaka kayan gona suna da arha a samu kuɗi a saye a aje sa anan an hi samun riba mai yawa sai a taimaka mai gida wajen tattalin iyali.
3. A yi kafa daidai da yawan masu bukata da kuma lokaci. Daga ƙawayya yamai yan cin rani masu yawa na tahowa yamai kenanakwai masaya. Ga damana ko duka yan cin rani komowa suke yi ƙawayyansu..
4. Wannan sana'a mata yan kasuwa na sayen ta waɗanda ba su da damar komawa gida.

Mata ne ke yin irin wannan sana'a don taimaka ma gajiyayyun maza. Da yan kuɗi kaɗan ana iya yin wannan sana'a.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP13 |  |
| Sana'a | Shinkafa da wake | |
| Gari | Yamai pudiriyer | |
| Kala | Sarafa kayan gona | |
| Sunan hausa | Shinkafa da wake | |

Kayan gami

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Wake rabin tiya : 275 F |  | Mai litir 3 : 1.950 F |
|  | Shinkafa kilo 5 1625 F |  | Tanka na 500F + gishiri na 50F + maji na 200F |
|  | Kanwa ta 25 F |  | Itacen dahuwa na 300 F |
|  | Ruwa na 50 F |  | Tumati na 500F |
| Jimilla : 5.475 F | | | |

Kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Tukunya 2 : 17.500 F |  | ƙaramar koshiya : 250 F |
|  | Mayan kwanoni 2 a 14 000 F |  | Dozin 2 na koshiya :5.000 F |
|  | Faranti 4 a 4.000 F |  | Tukunyar sanholama 5.000 F |
|  | Faranti 2 na ƙarhe 5000 F |  | Faranti ƙanana guda 35 : 3500 F |
|  | Banci 2 : 12.000 F |  | Babbar tebur 15.000 F |
|  | Bokiti 2 3.000 F |  | Manya robobi 2 14.000 F |

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | ƙananan robobi 2 : 3.000 F |  | Luddai na miya 100 F |
| Jimilla : 102.250 F | | | |

Yadda ake wake de shinkafa: tun da jijjibi ake dahuwa ƙarhe 3 – karhe 4 na sahe

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A hidda kazamtar da ke cikin wake da kuma shinkafa | Kar a bar tsakuwa ciki. A yi aiki da wake wanda baya da kwaro kwarai |
|  | A wanke wake sosai da ruwa | |
|  | A sa cikin tunkunya ya tafasa sa'anan a jefa kanwa kaɗan | A yi hankali kar a sa ruwa dayawa |
|  | In wake ya kusa dahuwa a zuba shinkafa a ruhe tukunya | |
|  | A yanka albasa, tumatir ɗanya a sa mai da gishiri da maji. | |

Yadda ake saidawa

| | | |
|---|---|---|
|  | A cikin kwanoni ko farantinnai ake saidawa. | |

A yi tunani tun farko don a tabbata da riba tana shigowa ko da a kwatace ne.

kuɗin kayan gami = 6.775 F
5.475 F
1.000 F = kuɗin takasi
300 F = na abinci

Yawan fala da aka yi:

Dahuwa 1, fala 120
120 x 100 = 12.000F

Lissahin riba :
in an saida fala 120
120 F × 100 = 12.000 F
12.000 F - 6.775 F = 5.225 F
Ciniki – Uwa = Riba

In an saida fala 67
100 F × 67 = 6.700 Fcfa
6.775 F - 6.700 F = 75 F : Riba ƙadan ce.

In an saida fala 60 :
100 F × 60 = 6.000 F
6.000 F – 6.775 F = - 775 F
Ciniki – Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. a yi lissahin da riba za ta shigo koda a misalce ne.
2. a sayi kayan haɗi tun suna arha kamar ga kaka, abinci ba ya da tsada, tiya ba ta wuce 250F, a haɗa kuɗi a saye a adana.
3. a yi wake da shinkafa daidai da masayan da a akwai da kuma lokaci.
   Ga rani an hi samun ciniki saboda yan cin rani na bar garuruwan su zo yamai neman aiki. Akwai ciniki wannan lokaci sosai saboda sun koma gida. A riƙa dahuwa tun da sahe ƙwarai saboda masu hitowa tun da sahe da yara masukarin sahiya.
4. a yi nazari don a san suwanene masaya.

Tun da yara ne a yi arhaa saida masu 50F. A saida a cikin lakkwal.
Sana'a ce mai amfani, mata ke yin ta don su taimaka mazansu gajiyayyu har su ruhe wasu ramce.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP14 |  |
| Sana'a | Nap | |
| Gari | Gidan artisana wadata | |
| Kala | Ɗumki nap | |
| Sunan hausa | Nap | |

Kayan gami

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Zare mai lamba 10 = 4800F |  | Gwam = 50 F |
| Jimilla : 4.850 F CFA | | | |

Kayan aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Allura limaro 9 = 150 F |  | Zane = 500 F |
| Jimilla : 650 F CFA | | | |

Ga yadda ake yin nap (kwana 14)

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A mallaki zare da allura ko kuroshe (awa1) | Zaren da za a zaɓa ya dangance da irin nap da za a yi. |
|  | A zaɓi zanen da yadace da nap | |
|  | A ɗauki kuroshe a yi ƙulli. A yi birji kewaye na farko, sa'anan na biyu (minti 15) | |
|  | A dubi zane sai a ba nap kama sai a ci gaba da ɗumki (minti 45) | Kar ayi ma nap dauɗa |
|  | A wanke nap kuma a sa mata gwam (minti 15) | A bari ta bushe ana yi ana jan ta don kama ta hito. |

Yadda ake saidawa

| | | |
|---|---|---|
|  | Ana saida nap kamar guda 7 ƙanana na salon da na tebur gabaɗaya. | A goge da kyau |

A yi tunani tun farko don a tabbata da lalle riba tana shigowa.

Kuɗin kayan gami :
4.850 F
400 F : na takasi
Jimilla : 5.250 F CFA

Yawan nap da aka ɗumka
Kwanhile 1

Lissahin riba :
In an saida kwanhile 1
15 .000 F cfa × 1 = 15.000 F cfa
15.000 F cfa – 5.250 F cfa = 9.750 F a cikin kwana 14 misali 695F kowane rana.
Ciniki – Uwa = Riba

In a cikin wata 3 za a saida kwanhile 1
15.000 F cfa – 5.250 F cfa = 9.750 F a cikin kwana 90 misali 108F a kowace rana : Riba kaɗan ce.

In a cikin wata 4 za a saida kwanhile 1
15.000 F cfa – 5.250 F cfa = 9.750 F kenan a cikin kwana 120 misali 80F kowace rana.

Idan ana son cin riba :

1. a yi lissahin da zai sa a ci riba ka da a kwatamce.
2. a iya ciniki don a samo zare mai kyau mai arha .
3. a yi nappopi dangance da na buƙata. Irin waɗannan kaya sai an yi komandinsu sa'anan a ɗumka su. A rage lokacin da aikin yake ɗanka, a maida shi kwana 10 kambaci kwana 15.
4. a yi tunani don a sa su wanene masaya. Mata ne amare ke saye, a sami tsarin da za a sami masu yaba aiki a ko'ina, wurin bukukuwa a cikin unguwowi.

Sana'a ce wadda yan mata amare don ɓata lokacin. Tana taimakawa wajen yi ma gida ado har a sami yan kuɗi na biyan buƙata.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP15 |  |
| Sana'a | Saida hura | |
| Gari | Yamai pudiriyer | |
| Kala | Sarafa kayan gona | |
| Sunan hausa | Hura | |

Kayan gami

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Tiya 9 na hatsi = 4.050 F |  | Kashin itace = 300 F |
|  | Tanka = 50 F |  | Ruwa = 30 F |
|  | Wasu yazuzzuka kala-kala = 100F |  | Sukari karo = 30 F |
|  | Nono = 750 F |  | Niuka = 225 F |
| Jimilla : 5.360 F CFA | | | |

Kayayyaki aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Turmi da taɓarya = 5.500 F |  | Tukunya = 14.500 F |
|  | Kwarya 6 = 3.000 F |  | Bokiti 3 = 3.000 F |
|  | Babbar koshiya = 375 F |  | Luddai = 275 F |
|  | ƙaramar tasa ta roba 270 F |  | Babbar tasa = 850 F |
|  | Tame 1 = 500 F | | |
| Jimilla : 28.270 F CFA | | | |

Ga yadda ake yin hura:

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A surhe hatsi a hidda dussa | |
|  | A hece dussa da faifai (awa1) | |
|  | A ƙashire hatsi a ribɗe (awa 1) | A leɓeye da kyau |
| | A daka yazuzzuka (minti 10) | |
| | A sda tame a reraye | |
| | A yi mulamulan dawo ba a sa ruwa cikin dawo | |
| | A jefa dawo a tukunya (awa 2) | |
| | A hiddo dawo daga tukunya a farfasa shi (minti 30) | |
| | A saɓe dawo (minti 30) | Kar a sa ruwa dayawa |
| | A yi dunkƙule-dunƙule na saidawa | |

Yadda ake saidawa

| | | |
|---|---|---|
|  | Dunƙule-dunƙule aka saidawa. Sai a sa nono, sukari, ruwa sai a dame a sha da luddai | Ana sa galas ga masu hali |

A yi tunani dan a san in an hidda uwa ana samun riba.

Kuɗin kayan gami :
5.360 F
400 F na abinci
Jimilla : 5.760 F

Yawan hurar da aka yi
Ɗan dawo : 250

Lissahin riba
In za a saida ɗan dawo 250,
25 F × 250 = 6.250 F
6.250 F - 5.760 F = 490 F
Ciniki – Uwa = Riba

In ɗan dawo 230 aka saida
25 F × 230 = 5.750 F
5.750 F - 5.760 F = 10 Fcfa
Ciniki – Uwa = Riba kaɗan ce.

In ɗan dawo 125 anka saida :
25 F × 125 = 3.125 F
3.125 F - 5.760 = - 2.635 F
Ciniki – Uwa = Faɗuwa

In ana son cin riba :

1. a yi lissahin da riba za ta sami ko da a kwatamce ne.
2. a sayi kayan gami tun suna da arha. Kuɗin hatsi yana canzawa daga 250F yana iya kai 750F in anka haɗa yan kuɗi sai a saye a adana don hatshi ba ya saurin ɓaci. In hatsi yana tsada sai a rage hannu wajen mulmula ɗiyan dawo.
3. a yi hura daidai da buƙatar masaya. A lokacin rani mutane dayawa na tahowa birni neman aiki. Mutanen nan ba su tahowa da iyalinsu kenan sai sun saye hura. Ga damana babu ciniki saboda kowa ya koma gida, a daidaita yawan hura za a yi da masayan wannan lokaci.

Sana'a ce da mata ke yi amma tsohi. Tana sa biya ma iyallai wasu buƙatu na yan da kullum.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP16 |  |
| Sana'a | Masar hatsi | |
| Gari | Kasuwar bonkanai | |
| Kala | Tuyar masar hatsi da saidawa | |
| Sunan hausa | Masar hatsi | |

Kayan hadi ( suna、yawa、da parashi )

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Tiya 5 na hatsi = 3.000 F |  | Goriba = 300 F |
|  | Ƙullin sukari = 175 F |  | Kanwa = 25 F |
|  | Gishiri = 50 F |  | Litir 2 na mai dinor = 1.400 F |
|  | Kashi itace = 400 F |  | ƙullin tanka = 200 F |
|  | Maji = 50 F |  | ƙuli-ƙuli = 350 F |
|  | Tumatir = 150 F |  | ɗan albasa = 50 F |
| Jimilla : 6.200 F CFA. | | | |

Kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Murhu da kasko = 3.000 F |  | Koshiya mai faɗi = 150 F |
|  | Luddai = 100 F |  | Koshiya ƙarama 150 F |

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Kwano na roba 12 = 1.200 F |  | Babbaor roba = 3.000 F |
|  | ƙwarya 2 = 1.500 F |  | Bokiti na roba = 1.000 F |
|  | Faranti babba = 1.500 F | | |
| Jimilla : 11.600 F CFA. | | | |

Yadda ake masa (kwana 2)

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A surhe hatsi (awa 1 da rabi) | |
|  | A bakice hatsi da ta tame ko faifai (minti 30) | |
|  | A ƙashire a ribɗe (awa 2) | A hidda tsakwa da ke ƙasa |
|  | A tankaɗe gari (minti 20) | |
|  | A daka goriba a sa ta cikin kwarya mai hudodi ta yi ɗiga (awa 1) | |

| | | |
|---|---|---|
|  | Ruwan nan na goriba a tafasa su a wuta (awa 1) | |
|  | A zuba tsaki cikin ruwan goriba don a sami kunu mai zaƙi (2h) | |
|  | A dama dawon don ya tahi bai ɗaya a aje dare ɗaya (awa 5) | A ruhe da kyau maganin ƙura |
|  | Da sahe a motsa dawon ana sa kanwa magani yami a sa sukari da gishiri da albasa (minti 30) | |
|  | Da luddai sai ana ɗebowa ama zubawa ga kasko ama masa (awa 4) | Kar a yi sake ta ƙone |

Yadda ake saidawa

| | | |
|---|---|---|
|  | Ana cin masa da tanka mai ƙuli-ƙuli da miya mai tumati. Ana cin ta da malku | Ana sa ta cikin tasa ko faranti |

A yi tunani don a san riba za ta shigo tun kahin a fara sana'a.

kuɗin kayan haɗi
6.200 F
300 F: na abinci
Jimilla : 6.500 F

Yawan masa da aka toya :

10 F × 1000 = 10.000 F cfa

Lissahin riba :
In an saida guda 1000
10 F cfa × 1000 = 10.000 F cfa

10.000 F cfa - 6.500 F CFA = 3.500 F cfa
Ciniki – Uwa = Riba

In guda 650 aka saida
10 F × 650 = 6.500 F
6.500 F CFA - 6.500 F cfa = 0 F ba riba

In guda 500 aka saida
10 F cfa × 500 = 5.000 F cfa
5.000 F cfa - 6.500 F CFA = - 1.500 Fcfa
Ciniki – Uwa = Faɗuwa

Don haka, in ana son cin riba :

1. a lissahi tun farko a tabbata ko da a kwatamce ne da lalle akwai riba.
2. a sayi kayan gami tun lokacin da suke arha. kuɗin hatsi hawa yake yi daga 250F zuwa 600F. In an fara yan kuɗi sai a saye su ga kaka.
3. a riƙa yin masa daidai da yawan masaya. A cikin garuruwa, mutane watsewa suke yi ga lokacin rani don haka a yi hankali kar a yi dawo a rasa masaya.
4. a yi nazari a san su wanene masaya in yara ne a yiu parashi da bai hi ƙarhi yara ba. In manya ne sai a yi ta dalla biyar (25F) ya zamanto kuma akwai mai saida nama ko malku a kusa. Ranar juma'a mutane dayawa na son yin sadakar masa ranar nan a ƙara ƙullun masa.
5. kar a yi tuya a rana a yi hankali kar a ƙone wkansa.

Wannan sana'a tsohin mata suka hi yin ta ko zaware ko kuma masu marayu da ke da nauyin cida gida. Da jalli kaɗan sai a yi wannan sana'a
Masa ana son ta ranar juma'a don sadaka, gidajen da ake yin ta yara da manya karyawa da ita.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP17 |  |
| Sana'a | A ci a sha ruwa / kwapto | |
| Gari | Kasuwar bonkanai | |
| Kala | Sarrafa abinci | |
| Sunan hausa | A ci a sha ruwa / kwapto | |

Kayan hadɗi (suna, yawa da parashi )

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Kunuwa itace tsanwa = 1.050 F. |  | Kashi icce 2 = 300 F |
|  | Rabi litir na mai = 325 f. |  | Ruwa = 25 f. |
|  | Gishiri = 50 f. |  | Tanka = 125 f. |
|  | Kanwa = 25 F |  | Maji = 75 F. |
|  | ɗan albasa = 50 F |  | ƙuli-ƙuli na gujjiya = 300 F |
| Jimilla : 2.325 F CFA. | | | |

Kayayyaki aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Tukunya = 10.000 F. |  | Roba 2 = 3.500 F. |
|  | Babba koshiya = 2.000 F. |  | Faranti 2 = 2.000 F. |
|  | Bokiti 1 = 1.000 F. |  | Leda = 150 F |

| | |
|---|---|
|  | Kwanoni 12 = 1.200 F. |
| Jimilla: 19.850 F CFA. | |

Yadda ake yin kwapto

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A tsintse ƙazantar da ta ciki ganye (awa 1) | A gyara da kyau |
| | A wanke ganye (minti 5) | |
|  | A hura wuta a aza ganye bisa wuta a sa kanwa (awa 3 – 4) | |
| | A sabke a sa cikin wani kwano | |
| | A ruhe da leda da babban tire don kar ya huce (minti 15) | |
|  | A daka ƙuli-ƙuli tanka, maji da gishiri (minti 15) | |
|  | A soya mai da albasa (minti 10) | |

Yadda ake saidawa

| | | |
|---|---|---|
|  | Cikin babban faranti a warwara mai a aza albasa sama | |

A yi tunani don a yi yadda riba za ta shigo.

Kuɗin kayan haɗi
2.325 F

Yawan abinda aka saida .
Fala 45

Lissahin riba:
In an saida duka fala 45 na kwapto
100 F × 45 = 4.500 F
4.500 F – 2.325 F = 2.175 F
Ciniki – Uwa = Riba .

In fala 24 aka saida
100 F × 24 = 2.400 F
2.400 F – 2.325 F = 75 F riba kaɗan ce..

In fala 20 aka saida
100 F × 20 = 2.000 F
2.000 F – 2.325 F = - 325 F.
Ciniki – Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba:

1. a yi lissahi na tabbatar da riba ko da a kwatamce ne;
2. a yi daidai yawan ciniki;
3. a san su wanene masaya;

wannan irin sana'a yan mata ke yin da shakala waɗanda mazansu ba su da ƙarhi sosai. Da kuɗi kaɗen sai a yi wannan sana'a.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP18 |  |
| Sana'a | Saida kihi soyayye | |
| Gari | Kasuwar bonkanai | |
| Kala | Kasuwanci kihi soyaye | |
| Sunan hausa | Saida kihi soyayye | |

Kayan haɗi (suna, yawa, parashi )

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Kilo 7 na kihi ɗanye = 5.000 F. |  | Itace = 200 F |
|  | Litir 3 da rai = 2.250 F. |  | Garin fulawa = 325 f. |
|  | Gishiri = 100 f. |  | Tanka = 300 f. |
|  | Maji 3 = 200 F. | | |
| Jimilla : 8.375 F CFA. | | | |

Kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Kasko = 650 F. |  | Matarari = 250 F. |
|  | Buhu yamti = 100 F. |  | Kwano da tire = 2.000 F. |
|  | Roba = 250 F. |  | Tabarma = 500 F |
|  | Murhun zamani = 500 F. |  | Bokiti na ƙarhe = 2.000 F. |
| Jimilla : 6.250 F CFA. | | | |

Yadda ake gyaran kihi

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A wanke kihi (awa 1) | A karkare da kyau a hidda ƙazamta |
|  | A sa garin fulawa kaɗan a shanya bisa tabarma shi bushe (awa 2 da rabi) | Kar a shanya ga rana |
|  | a kunna wuta a sa mai cikin kasko (minti 10) | |
|  | A sa kihi in mai ya yi zahi sosai (awa 4) | A bari ya soyu da kyau don in ba haka warti zai yi |
|  | A daka tanka (minti 30) | |

Yadda ake saidawa

| | |
|---|---|
|  | A sa cikin takarda a sanya tanka. |

A yi tunanikahin a soma sana'a saboda a haƙiƙance da akwai riba.

Kuɗin kayan haɗi
8.375 F

Lissahin riba :
In an saida kihin duka a cikin kwana 2
25 F cfa × 160 = 4.000 Fcfa
35 F cfa x 100 = 3.500 Fcfa
50 F cfa x 50 = 2.500 F CFA
100 F cfa x 20 = 2.000 F CFA
Jimilla : 12.000 F CFA
12.000 F – 8.375 F = 3.625 F.
Ciniki – Uwa = Riba

In kihin 25F, 50F déa 100F ne za a saida
25 F cfa × 160 = 4.000 Fcfa
50 F cfa x 50 = 2.500 F CFA
100 F cfa x 20 = 2.000 F CFA
Jimilla : 8.500 F CFA,
8.500 F – 8.375 F = 125 F
Ciniki – Uwa = babu Riba

In rabin kihin nan aka saida (165)
25 F cfa × 80 = 2.000 Fcfa
35 F cfa x 50 = 1.750 Fcfa
50 F cfa x 25 = 1.250 F CFA
100 F cfa x 10 = 1.000 F CFA
Jimilla : 6.000 F CFA
6.000 F – 8.375 F = 2.375 F.
Ciniki – Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. a yi lissahi don a tabbata da riba na shigowa ko da a kwatamce ne.
2. dan tsoron kihin yaɓaci ana iya sayen wanda ake iya saidawa rana ɗaya.
3. a daidaita yawan kihin da za a saidawa da yawan masaya. In yara masu ciniki a sayo kihi ƙanana kamar na 25F kihi na 100F ya hi ƙarhin yara ko da suna da 100F sun hi son su sayi wani abu da ita amma ba ɗan kihi guda tak ba.
4. a yi su wanene masaya. In yara ne a rahe parashin don yara su saye kuma a soya lokacin da mutane su ke buƙata.
5. da wannan sana'a ana samun ribar da za a biya ma iyali buƙatun sayen kaya lakkwal lahiya abinci tufaya da sauransu. Tana sa yara su yi maganin yinwa tsakanin 12 na rana da ƙarhe 8 na dare.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP19 |  |
| Sana'a | Yin turaren wuta | |
| Gari | Yamai banizumbu | |
| Kala | Yin turaren wuta da saidawa | |
| Sunan hausa | Yin turaren wuta | |

Kayan hadī

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Iccen turare kilo 1 = 1.500 F |  | Ruwan turare « harouna » = 450 F |
|  | Sarkin turare = 450 F |  | Ruwan turare « mutaka » = 450 F |
|  | Sandatir = 500 F |  | Ruwa turare kolonyi = 1.250 F |
|  | Marakana = 600 F |  | Girai ko ƙwaro = 250 F |
|  | Sukari = 250 F |  | Itacce dahuwa = 100 F |
|  | Kwalabe yamti 11 a 825 F | | |
| Jimilla : 6.675 F | | | |

Kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Bokit = 750 F |  | Murhu = 750 F |
|  | Yuƙa = 400 F |  | Tukunya = 3.000 F |

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Paniye = 500 F |  | Ispatil (iccen motsawa) 200 almakashi |
| Jimilla : 5.100 F CFA. | | | |

Yadda ake yin turare wuta

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A sa iccen turare cikin bokiti (minti 2) | |
|  | A sa ruwan turare kala da aka ambato (minti 5) | A cakuɗa sosai a bari sai awazu |
|  | A kunna wuta a aza tukunya (minti 5) | |
|  | A sa jira da sukari a cikin tukunya (minti 20) | |
|  | A zuba itaccen turare da suka kwana cikin ruwan turare kala-kala a motsa | |
|  | A motsa kaɗan-kaɗan har itatuwan turare su koma ja-wur. | |
|  | A zuba turaren cikin bokiti. | |

Yadda aka saidawa

| | | |
|---|---|---|
|  | A sa cikin kwalabe sai a saida | |

A yi tunani tun kahi a fara sana'a don a tabbata ɗa za a ci riba.

kuɗin kayan gami :
6.675 F + kuɗin takasi 400 F = 7.075 F CFA

Yawan kwalaben da aka yi :
Kwalba 10 ƙanana, 1 babba

Lissahin riba bayan an saissuwa:

In an saida kwalba 11 duka :
1.500 F x 10 = 15.000 F
5.000 F x 1 = 5.000 F
Jimilla : 20.000 F CFA:
20.000 F – 7.075 F = 12.925 F CFA
Ciniki – Uwa = Riba

In kwalba 5 kanana aka saida
1.500 F x 5 = 7.500 F
7.500 F- 7.075 F soit 425 F ba riba dayawa
Kenan sai an saida hiye da haka

In kwalba 3 za a saida kawar
1.500 Fcfa × 3 = 4.500 Fcfa
4.500 Fcfa – 7.075 F = 2.575 Fcfa
Ciniki – Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. a yi lissahi wanda zai tabbatar da riba koda a kwatamce ne.
2. a yi turare daidai yawan ma buƙata da kuma lokaci, ba duka lokaci ake samu masaya masu yawa ba. An hin son shi ga damana da lokacin ɗari.

Sana'a ce da tsohi mata ke yi don taimaka ma gida da yara mata masu aure wajen saye kayan ɗaki. Turare abu wanda matan aure shakala ke so ƙwarai.

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | NP20 |  |
| Sana'a | Saida kayan ƙira ta itace (sassaƙa) | |
| Gari | Gidan kallo na yamai | |
| Kala | ƙira (aikin hannu) | |
| Sunan hausa | ƙere-ƙere na itace (sassaƙa) | |

kuɗin kayan gami

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Itatuwa = 170.000 F |  | Mai na shushana = 1.000 F |
| Jimilla : 171.000 F | | | |

Kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Tenayi 5 = 3500 zuwa 5.000F kowane |  | Tebur = 15.000 zuwa 20.000 F |
|  | Rabo 3 zuwa 6 a 7.500 zuwa 8.000 F |  | Zartu 8 daga 7.000 zuwa 8.000 F kowane |
|  | Takarda tsanwa 3 zuwa 10 = 1.000 F |  | Shifon : |
| Jimilla : 26.500 a 42.000 F | | | |

kuɗin saida na ƙere-ƙere

| | |
|---|---|
|  | Mace na ɗauke de ruwa : 3.500 - 5.000 F |
| | Mace mai rawa : 20.000 - 40.000 F |
| | Mace mai son maza : 30.000 F |
| | Bahillatani : 15.000 - 50.000 F |
| | Dorina : 80.000 F |
| | Giwa : 30.000 F |
| | Mai tunani : 20.000 F |
| | Gyado : 12.500 - 17.500 F |
| Jimilla : 51.000 F à 272.500 F | |

Yadda ake kasuwancin : guda – guda

| Hotuna | Lokaci | Bayani |
|---|---|---|
|  | Awon itatuwa (minti 10) | |
|  | A sassare itatuwa awa 1 da minti 30 | |
|  | A sassaƙe itatuwa a ba su kamar da ake so (kwana 1) | |
|  | A ba ta kamar da aka zaɓa (kwana 1) | |
|  | A yi mata sumul-sumul (kwana 1) | |
|  | A sa mata takarda (ini 1) | |
|  | A shafa mai na shushana | A shaye da kyau da shifon |

A yi tunani tun farko don a san lalle riba na shigowa.

kuɗin sayen kayan aiki
170.100 F

Kuɗin saidawa
51.000 F à 272.500 F

Lissahin riba bayan saisuwa

272.500 F cfa – 170.100 F cfa = 102.400 Fcfa
Ciniki – Uwa = Riba

Lissahin riba na 2 :
51.000 F Cfa – 170.100 F = - 119.100 F
Ciniki – Uwa = Faɗuwa mai yawa

Idan ana son cin riba

1. a yi lissahi don a sami riba ta shigo ko da a yi ɗan kwatamci ne.
2. a aikata itatuwan da kyau don a sai sassaƙa mai kyau.
3. a ƙere-ƙere na itatuwa masu yawa lokacin hutun yan lakkwal da kuma lokaci zakkuwa nasaru masu yawon buɗe ido, baƙi na son kayan ƙere-ƙere na ŋijar ƙwarai.

Wannan sana'a maƙéra icce (masassaƙa) ke yin ta a ŋijar. Masu saye wannan sana'a yan ƙasashen waje ne saboda addinin musulumci bai yarda ba da gumki ko mutun-mutuni ba.

Kundin ƙananan sana'o'i : ɗan kacare (mai saye ko saidawa guda-guda

| | | |
|---|---|---|
| Lamba | ND01 |  |
| Sana'a | Saida nono mai sanyi | |
| Gari | Yamai da'ira ta 3 | |
| Kala | Kayan da aka sarrafa | |
| Sunan hausa | Nono mai sanyi | |

Kayan gami (haɗi)

| | |
|---|---|
| | Bido 2 na litir 10 kowane a 2000F/bido |
| Jimilla | 4.000 F |

Kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Bidons 2 a 12.000 F |  | Butali yamti na litir 1 a 100F |
| Jimilla | : 12.100 F | | |

Yadda ake saidawa

| | |
|---|---|
|  | Ana saidawa litir 250 F |

Ayi lissahi kahin a fara sana'a don a sani bayan an hidda uwa ana iya samu riba sosai.

kuɗin kaya
4.000 F kuɗin kaya
50F kuɗin takis
Jimilla: 4050F

Madarar da aka saida
Bido na litir 20 a 6000F

Ƙissahin riba:
In an saida litir 20:
300 F × 20 l = 6.000 Fcfa
6.000 F – 4.050 F cfa = 1.950 Fcfa
Ciniki – Uwa = Riba

In an saida litir 13,5:
300 Fcfa × 13.5 L = 4.050 F
4.050 F – 4.050 F = 0 F babu riba kenan sai an saida hiya da haka.

In an saida litir 10 :
300 F × 10 = 3.000 F
3.000 F – 4.050 F = - 1.050 F
Ciniki – Uwa = Faɗuwa

Idan ana son a ci riba :

1. A yi lissahin da zai sa uwa ta hito har a ci riba.
2. A daidaita nonon da za'a saida da yawan masaya don kar ya yi saura.

Sana'a ce da matan hulani ke yi don biyan buƙatun iyallansu da bisashensu. An hi yin ta ga damana da ɗari.

| | | |
|---|---|---|
| No | ND02 |  |
| Sana'a | Saida goro | |
| Gari | Kasuwar bonkanay | |
| Kala | Kayan gona | |
| Sunan hausa | Tallar goro | |

Kuɗin kaya

| | |
|---|---|
| | Huhu 3 na goro 180.000 F |
| Jimilla 180.000 F | |

Kayan aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | ɗaurin takarda : 15.000 F |  | Tabarma : 500 F |
|  | Tebur : 10.000 F | | |
| Jimilla: 25.500 F | | | |

Yadda ake saidawa

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Guda-guda |  | Ƙwarya-ƙwarya cikin ledodi |
|  | Kashi-kashi | | |

Ayi tunani sosai kahin a soma sana'a don a sani tun farko da ana iya cin riba.

kuɗin sayo goro: 180.000 F
400 F CFA na abinci + 15.000 F na takarda + 2.000 F na abinci.
jimilla : 197.400 F CFA

yawan goron da aka saida:
huhu 3
lissahin riba:
in saida huhu 3 duka
70.000 F × 3 = 210.000 F
210.000 F – 197.400 F = 12.600 F
Cinikin - Uwa = Riba

In an saida huhu 2
70.000 F × 2 = 140.000 F
140.000 F – 197.400 F = - 57.400 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa
In an saida huhu 2,9
70.000 F × 2,9 = 203.000 F
203.000 F – 197.400 F = 5.600 F
Cinikin - Uwa = Riba kaɗan ce.

Idan ana son cin riba :

1. A yi lissahin da zai sa a ci riba ko da a misalce ne.
2. Ayi hankali kar goro ya bushe a adana da kyau.
3. A bar bada bashi don wasu ba su biya.

Sana'a ce da samari yan ƙauye suke yi in sun zo birane.

| No | ND03 |  |
|---|---|---|
| Sana'a | Saida itace | |
| Gari | Da'ira ta 3 yamai | |
| Kala | Kasuwanci | |
| Sunan hausa | Saida itace dahuwa | |

Kudin sayen itace

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Tuli 2 na itace 56 000F |  | hirɗe: 1.500F |
| Jimilla : 57.500 F CFA | | | |

Kayan aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Gatari 1.500 F |  | Babba leda ta ruhe itace 1.000F |
| Jimilla : 2.500 F | | | |

Yadda ake saidawa

| | |
|---|---|
|  | Kashi-kashi na 100 F. |

Ayi tunani sosai tun farko don a sani bayan an hidda uwa da riba mai tsoka za ta iya shigowa.

kuɗin sayen kaya (itace) : 57.500 F

yawan itace da aka saida: Tuli 2

lissahin riba in an saida duka tulin 2

35.000 F × 2 = 70.000 F
70.000 F – 57.500 F = 12.500 F
Cinikin - Uwa = Riba

In an saida tuli 1 da rabi
35.000 F × 1,5 = 525.00 F
52.500 F – 57.500 F = - 5.000 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

Idan ana son ci riba:

1. Ayi lissahin da zai sa a sami riba;
2. A kwatamta don ayi yadda ciniki zai ɗara kuɗin saye.

Sana'a ce da mafi yawa matan da ke cikin birane ke yi don biyan buƙatun iyali da sauransu. Itace suna saurin sayuwa har ma ga damana.

| | | |
|---|---|---|
| No | ND04 |  |
| Sana'a | Saida daudawa kalwa | |
| Gari | Yamai kasuwar ƙasa | |
| Kala | Kayan gona | |
| Sunan hausa | Saida daudawa kalwa | |

kuɗin sayen kaya

| | |
|---|---|
| Daudawa : ƙwarya 10 na kalwa (kowace guda 100) | 2.000 kowace ƙwarya 20.000 F |
| Jimilla 20.000 F | |

Kayan aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Roba babba 1.250 F |  | Leda ta ƙullawa a 2.500 F |
|  | Kwaryoyi 3.750 F |  | Tebur 3.000 F |
| Jimilla : 10.500 F | | | |

Yadda ake saidawa

| | |
|---|---|
| | Guda-guda |
| | Ana sa guda 100 (ƙwarya 1) a cikin leda ta 10F |

Ayi tunani kahin a soma sana'a don a sani bayan an hidda uwa da riba na iya shigowa.

kuɗin kaya: 2.000 F + na abinci + 50F na takis
Jimilla : 2.150F

Yawan daudawar da aka saida: Guda 100

Lissahin riba:
In an saida guda 100
25 F × 100 = 2.500 F
2.500 F – 2.150 F = 350 F
Cinikin - Uwa = Riba

In guda 86 aka saida
25 F × 86 = 2.150 F
2.150 F - 2.150 F = 0
Cinikin - Uwa = babu riba

In guda 50 aka saida
25 F x 50 = 1.250 F
1.250 F – 2.150 F = - 900 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. A yi lissahin da za a ci riba ko da akwatamce ne.
2. A sayi daudawar kalwa mai kyau.

Sana'a ce da tsohin mata ke yi don su sami abun sayen goro, gudummuwa da sauransu.

| | | |
|---|---|---|
| No | ND05 |  |
| Sana'a | Saida garin masara | |
| Gari | Yamai kasuwar ƙasa | |
| Kala | Sarrafa sana'a Kayan gona da saida shi | |
| Sunan hausa | Saida garin masara | |

Kayan hadi

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Buhun masara 15.000F |  | Kullin leda na 200F |
|  | Ruwa 100F | | |
| Jimilla: 15.300 F CFA | | | |

Kayayyaki aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Turmi da taɓarya 5.500F |  | Faifai 2 a 1.000F |
|  | Kwarya 2 1.500F |  | Bokiti 1.125F |
|  | Tabarmi 10 a 5.000F |  | Abubuwan sanya ruwa 4.500F |
|  | moɗa na roba 50F |  | matankaɗi 3 a 1.500F |
| Jimilla : 20.300 F CFA | | | |

Yadda ake yin gari

| Hotuna | Hanyoyi | Bayani |
|---|---|---|
|  | A surhe masara kuma a bakice. Ana iya kai mashin (awa 5) | |
|  | A tankaɗe da matankaɗi (awa 1) | |
|  | A ƙashire masara, a bari a jima kaɗa sai a rimbɗe a maida gari (awa 2) ana iya kai mashin | A hidda ƙasa (aleɓaye) |
|  | a tankaɗe a hidda gari lukwi-lukwi (awa1) | |
|  | A shanya gari bisa tabarmi ya bushe (awa1) | A yi hankali da ƙura |
|  | An sanya cikin ledodi a ƙulle sai a saida. | |

Yadda ake saisuwa

| | | |
|---|---|---|
|  | Ana saidawa ƙulli-ƙulli | |

A yi tunani kahin a soma sana'a don a sani in an hidda uwa ana samun riba.

Kashe-kashe:
15.300 F kuɗin kaya (masara)
1.500 F na niƙa
1.200 F na dako
150 F na takis
1.500 F CFA na abincin ranar nan
Jimilla : 19.650 F CFA ko 18.150 F

Yawan garin da aka ƙulla: leda 250F

Lissahin riba bayan saidawa
In an saida duka:
100 F × 250 = 25.000 F
25.000 F – 19.650 F = 5.350 F
Cinikin - Uwa = Riba

In an saida ƙulli 200
100 F × 200 = 20.000 F
20.000 F - 19.650 F = 350 F
Cinikin - Uwa = Riba kanɗan doli sai an saida hiye da haka

In an saida ƙulli 125
100 F × 125 = 12.500 F
12.500 F – 19.300 F = - 6.800 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. A yi lissahi wanda zai sa a ci riba ko da a misalce ne.
2. A sayi kayan gami tun suna da arha.

Kuɗin kaya canzawa suke yi tiya na iya kamawa daga 250F har 450F. Masara ba ta zahin ɓaci. Ana iya biyar kasuwowi don a saida garin.

3. A daidaita yawan garin da za'a ƙulla da yawan masaya.

A birni mutane masu yawa basu da kayan aiki da lokacin na su yi garin masara, mutane sun hi son su sayi garin.

Sana'a ce da mata ƙadai ke yin ta don biyan buƙatunsu da na iyalinsu. Da kuɗi kaɗan sai a yi wannan sana'a kuma ana samun riba mai dama-dama.

| | | |
|---|---|---|
| No | ND06 |  |
| Sana'a | Saida kwambitar | |
| Gari | kasuwar kasa Yamai | |
| Kala | Sana'a Kayan gona | |
| Sunan hausa | Saida kwambitar | |

Kuɗin saye

| | |
|---|---|
|  | Buhu 5 na kilo 50 a 50.000F, kilo1 200F |
| Jimilla : 50.000 F | |

Yadda ake saisuwa

| | |
|---|---|
|  | Kilo-kilo |

A yi tunani tun farko kahin a fara sana'ar don a tabbatar da lalle riba na iya shigowa bayan an hidda kashe-kashe.
kuɗi kaya : 50.000 F
1.000 F na abinci.
50 F na takis
Jimilla : 51.050 F

Yawan kwambitar da aka saida: kilo 250

Lissahin riba:

In an ka saida kilo 250
325 F × 250 kg = 81.250 F
81.250 F – 51.050 F = 30.200 F
Cinikin - Uwa = Riba

In kilo 158 ne aka saida
325 F ×158 = 51.350 F
51.350 F – 51.050 F = 300 F
Cinikin - Uwa = Riba kaɗan ce.

In kilo 125 aka saida
325 F × 125 kg = 40.625 F
40.625 F –51.050 F = - 10.425 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. A yi lissahi na biɗa riba ko da ko a kwatamce ne.

A adana kayan da kyau.
A iya ciniki da masu saye don ana iya saida kilo hiye da 1.000F
Ga azumi ana son kwambitar sosai a yi tanadi don kar ya katse ga wannan lokaci.
Sana'a ce da samari yan ƙauye da ke zakkuwa birni ke yi don su sami abin kashi da na sayen tufafi. Sana'a ce da ke rage ma samari rishin aikin yi.

| | | |
|---|---|---|
| No | ND07 |  |
| Sana'a | Saida lemun zaƙi | |
| Gari | kasuwar bonkanai | |
| Kala | Kayan gona | |
| Sunan hausa | Saida lemun zaƙi | |

kuɗin saye lemu

| | |
|---|---|
| | Guda 200 a 2.000 F |
| Jimilla: 2.000 F | |

Kayan aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Kwarya 2 a 2.000 F |  | Babban kwano 1 1.500 F |
| Jimilla : 3.500 F | | | |

Yadda ake saidawa

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Guda-guda |  | Kashi-kashi |

A yi tunani kahin a soma sana'a don a tabbata da za'a ci riba:

kuɗi sayen lemu: 2.000 F + 100 F na abinci + 50F na takis ,= 2.150 F CFA

Yawan lemu da aka saida : guda 200

Lissahin riba :
In an saida guda 200
25 F × 200 = 5.000 F
5.000 F – 2.150 F = 2.850 F
Cinikin - Uwa = Riba

In guda 100 aka saida
25 F × 100 = 2.500 F
2.500 F – 2.150 F = 350 F
Cinikin - Uwa = Riba kaɗan ce

In guda 50 aka saida
25 F × 50 = 750 F
750 F – 2.150 F = - 1400 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. A yi lissahin da zai sa'a sami riba.

A sami lemu mai kyau, kar a yi sake lemun ya bushe.
Sana'a ce da samari da yan mata ɗiyan tallakawa ke yi don su biya wasu buƙatun. Sana'a ce maras wuya kuma da kuɗi kaɗan sai a yi ta. Samarin karkara na yin wannan sana'a idan suka zo birni.

| No | ND08 |  |
|---|---|---|
| Sana'a | Saida ruwan sanyi | |
| Gari | kasuwar bonkanai | |
| Kala | Kayan da aka sarrafa | |
| Sunan hausa | Saida ruwan sanyi | |

Kayan Hadi ( suna、 yawan kaya、 da parashi. )

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Litir 20 na ruwa 100F |  | Ledodi na kulla ruwan sanyi 700F |
| Jimilla: 800 F | | | |

Kayayyakin aiki

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Firigo : 300.000F |  | moda : 150 F |
|  | Bokiti 2 a 2.500 F |  | Tarmos 2 a 25.000 F |
| Jimilla : 327.650F | | | |

Yadda ake aikin ruwan sanyi

| Hotuna | |
|---|---|
|  | Kulla ruwan sanyi daidai-daidai a sanya cikin firigo |
|  | In sun yi sanyi sosai a hiddo a sa cikin tarmos a tahi talla |

Yadda ake saidawa

| | |
|---|---|
|  | Ana saidawa leda-leda. |

A yi tunani kahin a fara sana'a saboda a tabbata da ana iya cin riba.

Kuɗin sayen kaya: 800 F + 500F kuɗin wuta = 1.300F

Ruwan sanyi da aka saida : leda 200 a 10F = 2.000 F

Lissahin riba:
In an saida ƙulli 250
10 F × 200 = 2.000 F
2.000 F – 1.300 F = 700 F
Cinikin - Uwa = Riba

In leda 130 aka saida
10 F × 130 = 1.300 F
1.300 F –1.300 F = 0 F
Cinikin - Uwa = babu Riba ko kaɗan
In leda 50 aka saida

10 F × 50= 500 F
500 F – 1300 F = - 800 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. A yi lissahin da zai sa a ci riba ko da a kwatamce ne.
2. A ƙulla ruwan sanyi yadda ake iya saida su.
3. A san su wanene masu sayen ruwan sanyi. Ga zahi a yi ruwan sanyi diyawa. Kar a ƙulla ga lokacin sanyi.

Sana'a ce da mata ke yi lokacin zahi. Tana taimaka ma mata wajen biyan buƙatunsu na bukukuwan suna da aure har ma a aje wasu yan kuɗi ma.

| | | |
|---|---|---|
| No | ND09 |  |
| Sana'a | Saida tsintsiyar shara | |
| Gari | Yamai kallai ta kudu | |
| Kala | Kasuwanci | |
| Sunan hausa | Saida tsintsiya | |

kuɗin sayen tsintsiya

| | |
|---|---|
|  | Tsintsiya guda 100 a 50F guda |
| Jimilla : 5000F | |

kuɗin saidawa

| | |
|---|---|
| kuɗin saidawa : 10.000F | Tsintsiya 100 a 100F |

Yadda ake saidawa

| | |
|---|---|
|  | Ɗauri-ɗauri |

A yi tunani kahin a fara sana'a don a sani in an hidda uwa za a ci riba

Kuɗin saye: 5000F

Kuɗin saidawa : 10.000F

Lissahin riba:

In an saida tsintsiya 100
100Fcfa×100=10000Fcfa

10000Fcfa - 5000Fcfa =5000Fcfa
Cinikin - Uwa = Riba

In an saida tsintsiya 50
100Fcfa× 50=5000Fcfa

5000Fcfa - 5000Fcfa = 0Fcfa
Cinikin - Uwa = babu Riba sai an saida hiye da haka

In an saida guda 25
100Fcfa×25=2500Fcfa

2500Fcfa - 5000Fcfa = - 2500Fcfa
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. A yi lissahi da za a nemi riba koda a kwatamce ne
2. A sayi tsintsiya tun ba ta yi tsada ba.

Wannan sana'a tshohi mata ke yin ta na karkara da matan ƙabilar yarabawa. Kaɗan-kaɗan ne ake saidawa don haka ake gamawa da wata sana'a in ana son a hita.

| | | |
|---|---|---|
| No | ND10 |  |
| Sana'a | Saida cimaka | |
| Gari | Kasuwar bonkanai | |
| Kala | Kayan gona | |
| Sunan hausa | Saida cimaka | |

Kuɗin sayen hatsi

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Buhun hatsi 1 na kilo 100 a 16.500F |  | Buhun masara 1 na kilo 100 a 15.000F |
|  | Buhun shinkafa 1 na kilo 50 a 15.000F | | |
| Jimilla: 46.500 F | | | |

Kuɗin saidawa

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Buhun hatsi 1 na kilo 100 a 17.500F |  | Buhun masara 1 na kilo 100 a 16.000F |
|  | Buhun shinkafa 1 na kilo 50 a 16.000F | | |
| Jimilla : 49.500 F | | | |

Saisuwar ana yin ta a ƙalla buhu 1 na hatsi na kilo 100, buhu na masara na kilo 100 da buhun shikafa na kilo 50.

A yi tunani sosai kahin a fara sana'a don a haƙiƙance da lalle riba za ta shigo.

Kuɗin sayen kaya : 46.500 F + 100F na takis = 46600F

Yawan abinda aka saida:
Buhu 1 hatsi + buhu 1 na shinkafa + buhu 1 na masara = 58 000F

Lissahin riba

In an saida duka:
58.000 F – 46.600 F = 11.400 F
Cinikin - Uwa = Riba

In an saida rabi
29.000 F – 46.600 F = - 11400 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. A yi lissahin hiddo riba ko da a ciki kwatamci ne.
2. A sayi cimakar ga lokacin kaka.

Sana'a ce da maza ke yi wanda ake kira yan kasuwa masu saidawa a ƙasashen waje kuma su sayo daga ƙasashen waje. Sana'a ce mai buƙatar babba jalli don haka ba duk kowa ke rungumar irin wannan sana'a ba. Dan kasuwar cimaka babban mutun a cikin gari saboda mai bankin abinci ne na gari.

Kundin sna'o'i : Dila

| | | |
|---|---|---|
| No | NG01 |  |
| Sana'a | Saida kayan fata | |
| Gari | Gidan artisana wadata yamai | |
| Kala | Kirar fata | |
| Sunan hausa | Saida kayan fata | |

Kuɗin sayen kaya

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Takalmi daga 2.500F zuwa 12.000F |  | Bage 2.000F ko 17.000F |
|  | Poshat da1.000F zuwa 2000F<br>Potikile 250F zuwa 900F<br>Santir 1.500 zuwa 3000F | | |
|  | Puf 12.500F<br>Matashinkay3.000F zuwa 3.500F |  | Albbai 2.000F ko 7.000F |

Kayan aiki :

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Babbar tebur 10.000F |  | Runfa 8.650F |
| Jimilla: 18.650 F | | | |

Yadda ake saidawa

| | |
|---|---|
|  | Ana saidawa dayawa gabaɗaya ko rabin dozin in takalmi ne. |

A yi tunani tun ba a fara sana'a ba don a sani tabbat da riba na shigowa

Kuɗin kayan haɗi : 14.625F + 400 kuɗin takasi + 1000F na abinci
Jimilla: 16.025F

Yawan abinda ake ƙera: takin takalmi balka 5 x 6.250 F = 31.250 F

Lissahin riba:
In an saida takin 5
31.250 F – 16.025 F =15.225 F
Cinikin - Uwa = Riba

In taki 2 aka saida
6.250 F × 2 = 12.500 F
12.500 F – 16.025 F = - 3.525 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. A yi lissahi wanda riba za ta samu ko da cikin misali ne.
2. A sayi kayan aiki lokacin da suke arha.
3. A yi takalma daidai da buƙatar waɗanda suka tambaya.
4. A yi amfani da fata mai kyau.
5. A saida lokacin salloli da lokacinkasuwar baza koli.

Sana'a ce da mafi yawa maza ke yin ta amma ana samun mata kaɗan masu yin ta. Tana taimakawa masu yinta.

| No | NG02 |
| --- | --- |
| Sana'a | Saida kwapto |
| Gari | Kasuwar bonkanai |
| Kala | Sarrafa abinci |
| Sunan hausa | Saida kwapto |



Kayan gami (suna, yawan kaya da parashi )

Kuɗin saye

| Sunan kaya | Yawan kaya | Parashin saye |
| --- | --- | --- |
| Zogala (yar makka) | Buhu 10 | 30.000F |
| Kauci | Buhu 20 | 20.000F |
| Jimilla | Buhu 30 | 50.000 F |

Kuɗin saidawa

| Sunan kaya | Yawan kaya | Kuɗin saidawa |
| --- | --- | --- |
| Zogala (yar makka) | Buhu 10 | 87.500 CFA. |
| Kauci | Buhu 20 | 50.000cfa. |
| Jimilla | Buhu 30 | 137.000 F |

Yadda ake saidawa



Kashi-kashi

A yi tunani kahin a fara sana'a don a tabbata da ana iya hidda uwa har a samu riba.

Kuɗin sayen kaya : 50.000 F

Yawan abinda aka saida : buhu 10 na zogala + buhu 20 na kauci + buhu

Lissahi riba :
In saida duka:
(8.750 F cfa × 10) + (5.000 F x 20) = 87.500 F +50.000 F =137.500 Fcfa
137.500 F – 50.000 F = 87.500 F cfa .
Cinikin - Uwa = Riba

In buhu 6 da rabi na kauci da buhu 2 na zogala aka saida
(8.750 F cfa × 2) + (5.000 FCFA x 6,5) = 17.500 F + 32.500 F = 50.000 Fcfa
50.000 F – 50.000 F = 0 F cfa :
Cinikin - Uwa = ba Riba
In buhu 1 na zogala da buhu 6 na kauci aka saida
(8.750 F cfa × 1) + (5.000 F CFA x 6) = 38.750 Fcfa
38.750 F – 50.000 F = - 11.250 F.
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

In ana son cin riba:

1. A yi lissahin da riba sai ta samu ko da a kwatamce ne.
2. A yi nazari su wanene masu saye
3. A yi tanadin kwapto tun ga kakarshi a adana (ga damana)

Sana'a ce da tsohin mata na bakin kogin Isa da wasu wurare na bakin ruwa ke yi in da ake noma yan makka sosai. Tana biya masu buƙatotunsu na yau da kullum.

| | | |
|---|---|---|
| No | NG03 |  |
| Sana'a | Saida sarƙoƙi | |
| Gari | Gidan artisana yamai | |
| Kala | Kasuwaci | |
| Sunan hausa | Saida sarƙoƙi | |

Kuɗin saida kaya (suna, yawa, parashi da sauransu )

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Ɗan warwaro 15 a 300.000 F |  | Zobe 100 a 200.000 F |
|  | Sarƙa 30 a 450.000 F |  | Takin yan kunnai 300 a 300.000 F |
|  | Kurwa 50 a 300.000 F | | |
| Jimilla | 1.550.000 F | | |

Kuɗin saye kaya

| | | |
|---|---|---|
|  | | Zobe 100 = 100.000 F<br>Warwaro 15 = 250.000 F |
|  | | Taki 300 na yan kunnai = 150.000 F<br>Sarƙa 30 = 300.000 F |
|  | | Kurwa 50 = 150.000 F |
| Jimilla : 950.000 F | | |

Yadda ake sidawa

| | | |
|---|---|---|
|  | | Guda-guda ko taki-taki |

A yi tunani kahin a soma sana'a don a sani tabbat riba na shigowa.

Kuɗin saye kaya: 950.000 F + 9000F kuɗin haya/wata
Jimilla : 959.000 F

Lissahin riba:
In an saida duk:
1.550.000 F – 959.000 F = 591.000 F
Cinikin - Uwa = Riba

In rabi aka saida :
775.000 F – 959.000 F = - 184.000 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. A yi lissahin riba sai ta shigo koda cikin misali ne.
2. A yi tunani wanne mai saye.
3. A yi ma kaya aikin ƙwarai.

Sana'a ce da maza kaɗai ke yin ta. Da kuɗin maras yawa sai a yi ta. Tana sa a ciyar da iyali har a biya wasu yan buƙatu ko da yake masu yin ta ba su da daraja ƙwarai a cikin al'umma.

| | | |
|---|---|---|
| No | NG04 |  |
| Sana'a | Saida kayanmiya | |
| Gari | Kasuwar bonkanai | |
| Kala | Kasuwaci | |
| Sunan hausa | Saida kayanmiya | |

Kuɗin saye kayanmiya

| | |
|---|---|
|   | Tanka manya buhu mai tiya 35 = 28.000F |
|   | Tanka ƙanana buhu mai tiya 37 = 37.000F |
|  | Daudawa tiya 1 = 2000F |
|   | Albasa buhu = 20.000F |
|   | Tumatir busassa buhu mai tiya 18 = 22.500F |
|   | Kimba buhu 1 mai tiya 55 = 43.000F |
|   | Taharnuwa buhu mai tiya 32 = 35.000F |

| | |
|---|---|
|  | Garin rogo buhu mai tiya 35 = 11.500F |
|  | Buhun ƙuliƙuli = 20.000F |
|  | Miya guro (kuɓewa) buhu mai tiya 50 = 45.000F |
| Jimilla : 264.500 F CFA | |

Kuɗin saidawa

| | |
|---|---|
| Tanka manya = 42.000F | Albasa = 26.000 F |
| Kuɓewa = 50.000 F | Tumatir busassa = 14.400 F |
| Tanka Kanana = 44.400 F | Kimba = 55.000 F |
| Daudawa = 2.500 F | Taharnuwa = 44.800 F |
| Garin rogo = 28.000 F | Kuliƙuli = 45.000 F |
| Jimilla 352.100 F | |

Yadda ake saidawa : kashi-kashi, guda-guda da ƙulli-ƙulli cikin leda.

A yi tunani kahin afara sana'a don a san lalle akwai riba.

Kuɗin sayen kaya: 264.500 F + 200F na takis + 400F na takasi + 600F na abionci.
Jimilla = 256.700F

Yawan abinda aka saida:
In an saida duka
Lissahin riba:
352.100 F – 265.700 F = 86.400 F.
Cinikin - Uwa = Riba

In an saida rabi
176.050 F – 265.700 F = - 89.650 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa kenan sai an saida hiye da rabi

Idan ana son cin rabi :

1. A yi lissahin da zai bada riba ko da a misalce ne.
2. A yi tunani kan wanene mai saye.
3. A sayi kayan tun suna arha kacak.
4. A sayi kaya masu kyau
5. A adana su da kyau.

Sana'a ce da maza ke yin ta saboda tana son jalli mai kabri, tana bada riba sasai, a biya ma iyali buƙatunsu har a ji daɗi sosai.

| No | NG05 |  |
|---|---|---|
| Sana'a | Saida kabewa | |
| Gari | Kasuwar wadata yamai | |
| Kala | Kayan gona | |
| Sunan hausa | Saida kabewa | |

Kuɗin saye

| | |
|---|---|
| Kwarya 50 / 100 kwarya | 5.000.000 F ƙwarya 100.000 F |
| Jimilla : 5.000.000 F | |

Hanya :
Ana sayowa a tasha kwalo-kwalo a bakin kogin Isa. Sai mu sanyo cikin motoci mu zo kasuwar wadata mu saida masu saida kayan miya ko kuma masu ci

Kuɗin saidawa

| | |
|---|---|
| Kwarya 50 mai ɗa 100 kowace | 6.000.000 F / 120.000 F kwarya |
| Jimilla : 6.000.000 F | |

Yadda ake saidawa

| | | | |
|---|---|---|---|
|  | Guda-guda |  | Kashi-kashi |

A yi tunani kahin a fara sana'a don a sani lalle riba za ta shigo.

kuɗin saye: 5.000.000 F + 100F na takis + 3000F na haya
Jimilla : 5.003.100F

Yawan kabewa da aka saida: ƙwarya 50 = 6.000.000 F

Lissahin riba
In an saida duk
6.000.000 F – 5.003.100 F = 996.900 F
Cinikin - Uwa = Riba

In ƙwarya 42 aka saida:
120.000 F × 42 = 5.040.000 F
5.040.000 F – 5.003.100 F = 36.900 F
Cinikin - Uwa = Riba kaɗan ce

In kwarya 40 aka saida
120.000 F × 40 = 4.800.000 F
4.800.000 F – 5.003.100 F = - 203.100 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. A yi lissahin da riba sai ta shigo
2. A kiyaye kar kabewa ta lallace
3. A saye ga kakarta a aje da kyau
4. wannan sana'a mutanen da ke bakin kogin isa ke yin ta. Tana sauƙaƙa ma mata tahiyar bakin isa sayen kabewa.

Sana'a ce mai hatsari saboda kabewa saurin lalacewa take yi.

| | |
|---|---|
| No | NG06 |
| Sana'a | Saida albasa |
| Gari | Kasuwar ƙasa |
| Kala | Kayan gona |
| Sunan hausa | Saida albasa |



Kuɗin saye



| | |
|---|---|
| Albasa buhu 30 = | 135.000 F |
| Jimilla : 135.000 F | |

Yadda ake saidawa



Kashi-kashi ko kwano-kwano



Guda-guda

A yi tunani kahin a fara sana'ar don a tabbata da lalle ana iya cin riba.

Kuɗin sayen kaya: 135.000F + 500F na takis +500F abinci + 400F na takasi
Jimilla: 136.400 F

Yawan abinda aka saida : Buhu 30 na albasa

Lissahin riba:
In an saida duka:
8000 F × 30 = 240.000 F
240.000 F – 136.400F = 103.600 F
Cinikin - Uwa = Riba

In buhu 17,5 aka saida
8000 F × 17,5 = 140.000 F
140.000 F – 136.400 F = 3.600 F
Cinikin - Uwa = Riba kaɗan ce.

In an saida buhu 15
8.000 F x 15 = 120.000 F
120.000 F – 136.400 F = - 16.400 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

Idan ana son cin riba :

1. A yi lissahin da zai sa riba ta shigo ko da da kwatamci ne.

A saye lokacin da tana da sauƙi kuma a saida ga damana lokacin da take tsada inda buhu yana kai 16.000F
A samu dubara mai kyau ta ajiyar albasa har lokacin da ta yi wuya ƙwarai.

| No | NG07 |  |
| --- | --- | --- |
| Sana'a | Saida doya (dundu) | |
| Gari | Kasuwar wadata yamai | |
| Kala | Kayan gona | |
| Sunan hausa | Saida doya (dundu) | |

Kuɗin saye

| Yawan dundu | Parashi |
| --- | --- |
| Guda 300 | 240.000 F |
| Jimilla : 240.000 F | |

Hanya:
A ƙasar Gana ake noma doya. Mayan yan kasuwar katako ke odar ta. Ƙananan (masu talla) yan kasuwa wajen su suke sarawa a bashi in sun saida su yi balas amma sai an bada kamu ciniki.

Yadda ake saidawa

| | | | |
| --- | --- | --- | --- |
|  | Guda-guda |  | Kashi-kashi |

A yi tunani kahin a soma sana'a saboda a haƙiƙance da ana iya samu riba.

Kuɗin sayen dundu: 240.000 F + 1000F na abinci + 100F na takis + 1500F na haya.
Jimilla : 242.600F

Yawan dundu aka saida: guda 300

Lissahin riba
In an saida duka
1.000 F × 300 = 300.000 F
300.000 F – 242.600 F = 57.400 F
Cinikin - Uwa = Riba

In rabi ne aka saida
1.000 F ×150 = 150.000 F
150.000 F – 300.000 F = - 150.000 F
Cinikin - Uwa = Faɗuwa

In guda 243 aka saida
1.000 F × 243 = 243.000 F
243.000 F – 242.600 F = 400 F
Cinikin - Uwa = Riba kanan ce

In ana son cin riba
1. A yi lissahin sa zai sa riba ta samu ko da cikin kwatamci ne.
2. A adana dundun da kyau.
3. A iya ciniki da kyau wajen saye da wajen saidawa don a saida hiye da 1.000F guda ɗaya.
4. sana'a ce mai taimakawa mai yin ta wajen kula da iyalinsa. Amma tana son jalli mai kabri.

Sana'a ce da maza ke yi saboda ta na son kai da kawowa mai yawa.